♡💃YAN TIRIRRISHI 🐓💫
(_~Ajalin Kaza!!!~_)

*"When fate calls, will you answer?"*

Story And Written By;
Khadeejarth Sabi'u Yahyah
Nainarh KD, As you know me.
The Writer of;
1. SARAUNIYAR KYAU
2. ANEESERH (THE INNOCENT GIRL)
3. TSANTSAR SO
4. KIN CUCENI
5. RANAR BIYAN BUKATA
6. BA TABBAS
7. CAPTAIN AYUSHERH
8. ‘YAN TIRIRRISHI!

_A new blockbuster novel from the Nainarh KD the perfect pen, the story with the full of;_
# Love # Horror # Barkwanci
# Funny # Against The Perfect Exceptional Love!!💯💞💘

Free Book..From the beginning to the conclusion...💃💃💃
Dedicated to Maman Afrah..(Allah ya biya miki buƙatun ki na Alkhairi My ta musamman.🙏🤩

Copy is not allowed.¡!

Ba kuma zan Lamunci a canzan labari kota wata siga ba.¡!

_Assalamu Alaikum Jama'a barkanmu da sake kasancewa gaba ɗaya cikin wannan sabon tafiya mai cike da abin mamaki mai taken, ‘YAN TIRIRRISHI._
_Godiya ga Allah SWT da ya bani aron lokaci ya kuma bani ikon kammala littatafaina a baya, sannan ya nufe ni da fara wannan duka cikin iko da amincewarsa._

_‘YAN TIRIRRISHI labari ne mai ɗauke da sabon salo da kuma abubuwa da dama cikinsa yana kuma tafe da sinƙi-sinƙin Barkwanci faɗakarwa nishaɗantarwa da kuma uwa uba jan hankali

musamman ga wasu matan da kishi yake rufe musu ido su aikata mummunar ta'asa ba tare da tunani a kan me kaje ya dawo ba. Allah ya sa mu amfana da abin da labarin ke tafe da shi. Allahumma Ameen._

Perfectly Pen's 🖊️

Meet the amazing stories from the perfect writer's, Perfectly Pen's....

1. ‘YAN TIRIRRISHI
   By Nainarh KD
2. SHIRYAYYIYAR KADDARA
   By Queen Kainart
3. BAKIN SHAFI
   By OumYasmeen.

Official THRILLER...💥

https://chat.whatsapp.com/ICXo7IragdJBkz13G5ex9G

Title: ♡‘YAN TIRIRRISHI!♡

Author: NainarhKD

🔥👽...Life as a Monster or Die as Human...💥❤️

Genre: Horror, Action, Comedy, Dystopian, Zombie Apocalypse

Tagline: "Survival comes at a deadly cost"

Description:

In a world overrun by the undead, humanity teeters on the brink of extinction.

______

Wani irin kuka Miemie ta fashe da shi lokaci guda kuma suna ƙanƙame juna ita da 'Yar Gwal da ita ma hankalinta yake a mugun tashe ganin wannan tashin hankali da tun da uwarta ta haifeta bata taɓa gani ba.

"Innalillahi wayyo Allah na shiga uku ya tashi jama'a tashi ya yi fa!"

Rabi'ah ta faɗa a matuƙar ruɗe idanu warwaje take duban wannan mutumin da ya fara motsi jikinsa yana wani irin makwashewa ƙasusuwansa suna bada wani sauti lokaci guda fuskarsa ya koma wani irin abin tsoro ga saitin wurin da a ka cizesan ya yi wani mugun rami yana fitar da wani wawwaran jini.

"Shima fa Zombie'n ya zama wayyo Allah!"

Haleema ta sake faɗa cikin tsananin tashin hankali tana ƙamewa wuri guda ta ma kasa motsi bare tunanin gudun ceton rai.

Wani irin hautsinewa ƴaƴan cikin 'Yar Gwal suka yi ganin mummunar halittar da Mutumin ya koma da kuma jin abin da Haleema ta faɗa rashin abin yi da kuma tashin hankali ya sa ta ɗafale bayan Miemie ba tare da ta sani ba tana sakin wani marayan kuka....

---

"Sannunku da ƙoƙari kuzo mu ƙari sa ciki."

Cewar Haleema tana murmushi. Rabi'ah da ta juya baya tana ƙare ma garin kallo da gaba ɗaya bai fi ta ƙirga yawan gine-ginen ciki ba acewarta ta juyo tana ya mutsa fuska tare da buɗe baki zatayi magana daidai lokacin kuma 'Yar Gwal ta fito daga cikin gidansu a guje hannunta riƙe da kwalla mai ɗauke da manja Iya Sahu ta biyota ita kuma 'Yar Gwal da batasan da Mutum gabanta ba gadan-gadan ta nufo saitin da Rabi'ah da juyowarta ke nan take ai kuwa tun kafin Rabi'ah ta yi wani yunƙuri tuni aikin gama ya gama domin daga kwallar mai ɗauke da manjan har Manjan dake cike sama suka yi gaba ɗaya sannan da suka tashi yowa ƙasa basuyi masauki a ko'ina ba sai saman fuskar Rabi'ah Manjan gaba ɗaya ya wanke ma ta fuska sannan ya wanke farin Hijjabin jikinta yayin da sai da kwallar ta bugi goshin Rabi'ah sannan ta faɗi ƙasa, Rabi'ah bata gama tantance abin da ke wakana a duniyarta ba ita ma 'Yar Gwal da Marmara ne ta taka ya sa ta yi wannan aika-aika ta faɗa jikin Rabi'ah ita ma ta sama nata rabon na manja sai gaba ɗayansu suka yi ƙasa ji kake tim! Sun faɗi , Rabi'ah ta saki ƙarar azaba tana dafe kwankwaso.

---

"Wayyo Allah Mommy! Kizo ki taimakeni tsoro nake ji wannan wacce irin masifa ce mutane da an cije su sai dai su koma Zombie's gari ya koma tamkar maƙabarta!"

Cikin wani irin matsanancin kuka Miemie take wannan maganar hawaye nayi ma ta zarya kamar ba gobe.

Kallonta Rabi'ah ta yi wannan karon bataji haushinta ba ko kaɗan sai ma tausayi da ta bata hakan ya sa ta ɗan rungumota tana lallashi.

____

♡♡♡♡

Tafiya suka yi mai nisa daga wuraren da suke duk domin taya ƙawarsu murnar aurenta shi ya sa suka yarda suka yi kasadar biyota wannan wuri da sunan su ɗin ʻYAN TIRIRRISHI ne sai dai kwatsam ba tare da sanin dalili ko mafara ba sun tsinci kansu cikin wata iriyar duniya mai cike da abin tsoro yayin da wata mummunar cuta ta yaɗu ba wai cuta ba ce da a ke samu ta numfashi ko iska ko wani abu makarancin haka wannan daban ne wasu irin halitta ne na matattu mutane da suke komawa ZOMBIE da sun cije Mutum cikin lokaci ƙanƙani komai nashi yake sauyawa shima ya koma ZOMBIE. Ta ya kuke tunanin za su iya kuɓuta daga wannan masifa? Wai ma mene ne mafarar wannan masifar ne?
Ku biyo alƙalamin NainarhKD domin warware zare da a bawa.

🔥🔥🔥🔥🔥🔥🔥

When a mysterious virus turns people into ravenous zombies, the few remaining survivors must confront an unthinkable choice:

Become a monster to survive, or die as a human.

Follow the journey of a small group of survivors as they navigate the treacherous landscape of a zombie-infested world, confronting the darkness within themselves and the true horror of their new reality.

Questions for discussion:

1. Would you rather die as a human or become a zombie to survive?
2. How far would you go to protect your loved ones in a zombie apocalypse?
3. What does it mean to be human in a world gone mad?

Recommended for:

- Fans of zombie fiction and horror
- Those who enjoy dystopian and apocalyptic stories
- Readers looking for a thrilling and thought-provoking page-turner find out ƳAN TIRIRRISHI! (The Zombie Apocalypse) Special journey of life to survive, good plot, love, and Chaos....🔥

*بسم الله الرحمن الرحيم*

...01

Ragwajab kakeji lokacin da Motar ta tsaya cak ta bada wannan sauti.  A hankali ƴan matan suka fara saukowa daga Motar suna ya mutsa fuska kowacce da abin da ya dameta aƙalla za su kai su goma sha ɗaya.

Cikin ƙosawa Rabi'ah ta ce. “wai driver mun ƙari so garin ne da naga an tsaya ko ya ya?”
Ta ƙare maganar lokacin da ita ma ta sakko daga motar tana miƙa na gajiya, bata jira driver ya bata amsa ba ta kalla Haleema dake jingine da motar tana faman latsa waya ta ce. “Haleema wai me ke faruwa ne ya naga an sauke mu anan kuma ban ga alamun gidaje ba sai bishiyoyi....”

“karki damu ai mun kusa ƙari sawa, Suhaima ce ta nemi a tsaya wai fitsari takeji.”
Cewar Budurwar da Rabi'ah ta kira da Haleema tana yi ma ta nuni da wurin da Suhaima tabi.
Shiru Rabi'ah ta yi jin wacce a ka ambata, sai ta taɓe baki tare da jingina da motar tana ɗan kallon dajin har idonta ya sauka a kan ta, dariya ta ɗan yi sannan a fili ta ce.
“wai ke, ko dai dole kika ma waccan Yarinyarne a kan sai ta biyo mu?”

Ta faɗa tana taɓo Haleema tare da yi ma ta nuni da Wurin da Budurwar ta ware take zaune a takure sai lokacin Haleema ta lura ta ita dan a tunaninta bata fito daga Motar ba ma, girgiza kai Haleema ta yi. “bana son sa ido fa Rabi'ah yanzu mene ne ruwanki da ita?”
Rabi'ah tana ƴar dariya ta ce. “babu fa amma gani nayi sai kace wacce a ka yi ma dole a kan sai ta biyo mu...”
“ke dai kika sani.”
Cewar Haleema tana ci gaba da ƙoƙarin kiran lambar da take yi tun ɗazu sai dai saboda yanayin wurin da suke babu network ya sa kiran bata shiga.
Rabi'ah kuwa nutsuwa ta yi tana ƙirga yawan ƴan matan dariya na cinta faɗi take. “lallai kam gamu ‘YAN TIRIRRISHI mun faso gari wajen rai Goma lallai abin nayi ne...”

“ba goma ba ne mu goma sha ɗaya ne baki lura ba.”
Haleema ta katseta da faɗin hakan. “ai ke Amarya ce shi ya sa ban ƙirga dake ba.”
Rabi'ah ta faɗa tana gyara tsayuwarta jikin motar sakamakon hango Suhaima da ta yi ta tunkaro wurin.
“Ƴan Mata a koma mota muyi mu ƙari sa please.”
Haleema da ta hango Suhaima ita ma ta faɗa tana ƙoƙarin juyawa ta shiga Motar sai kuma ta tsaya tana kallon Rabi'ah da ta yi bake-bake jikin Motar daidai lokacin kuma Suhaima ta ƙari so wurin ba tare da ta kula kowa ba ta nufa hanyar shiga Motar sai dai Rabi'ah ta kare hanyar ba damar shiga.
“Malama bani hanya na wuce”
Suhaima ta faɗa ba tare da dubi Rabi'ah ba dan ta lura tun lokacin da suka baro Kaduna Yarinyar neman ta da faɗa take yi ita kuma ba zata biye ma ta ba domin a halin yanzu bata cikin hayyacinta sakamakon abin da ta gani ji take ma kamar ta fasa zuwa wannan ƙauyen da zasu je domin TIRIRRISHI sai dai idan ta tuna wacece Haleema a wurinta sai taji ba zata iya watsa ma ta ƙasa a ido ba gwara ta jira tun da zuwa gobe za su yi abin da ya kai su ana ɗaura Aure za su koma Kaduna.

“Rabi'ah bakijin ta ce ki bata hanya ta wuce ne?”
Haleema ta faɗa tana duban Rabi'ah.
“e naji sai dai jira nake ta maimaita dan banma ɗauka tana magana ba.”
Rabi'ah ta faɗa tana matsawa gefe dan dama cewa ta yi koda bala'i sai ta saka wannan ƴar iya yin ta yi magana kuma ta sakatan saboda haka burinta ya cika.

Suhaima bata ƙara cewa komai ba ta shiga Motar sauran ƴan matan ma duk suka shiga har da Amarya Haleema sannan driver ya ja Motar suka ɗauki hanyar ƙari sawa garin da suka nufa.

“ke dallah Malama kin ishemu da wannan koke-koken sai kace saceki zamuyi haba ko kuwa wani ne ya yi miki dole a kan sai kin biyomu wato ke ga kwaɗayayyiyar nama ko shi ne kin biyo ƴan tirirrishi saboda kici daɗi sai kace ba gidanku muka fara zuwa ba domin muyi tirirrishin a can amma kyatumarki ta yi mana ɗibar albarka har da haɗa mu da kare daga ƙarshe ma zani a hannu na samu na baro gidan naku ina sauke haki waiku masu gidan Gate kar a lalata muku....”

Rabi'ah ke wannan sababi babu ƙaƙƙautawa dama takaicin da mahaifiyar Yarinyar ta gumsa musu bai saketa ba gata ita kuma yanzu tazo ta wani ishesu da kukan banza.

Ɗiff Budurwar ta yi ta dakata da kukan duk da ba girme ma ta Rabi'ah ta yi ba hasali ma sai dai su zo sa'anni sai dai kasancewar Rabi'ah ɗin tana da ɗan girman jiki shi ya sa za'a ɗauka ta girme ma ta ne sosai.
“haba mana Rabi'ah Please ki barta taji da abin da takeji mana.”
Haleema ta faɗa cikin sanyin murya sannan ta kalla budurwar tare da faɗin. “sorry Please Miemie Rabi'ah ɗin ce sai a hankali.”
“a'a fa Haleema ki dena tare ma ta ai gwara Rabi'ahn ta cicci ma ta kina gani dai har da ita cikin masu yi mana kallon banza lokacin da muka je gidansu.”

Cewar wata daga cikin ƴan Matan mai suna Zieey.

“ya isa dai Dan Allah a bar maganar!.”

Haleema ta faɗa da son maganar ta ƙare a hakan dan har wani ciwon kai surutun nasu ya fara saka ma ta duk da dai gefe guda ita ma bataji daɗin abin da mahaifiyar Miemie ɗin ta yi musu ba sai dai ba yadda zatayi tun da Kanwar mahaifiyarta ce.

“ah maganar fa ba zata ƙare ba tsakani da Allah fa kina gani fa har yanzu ciwon da naji garin gudun ceton rai bai dena raɗaɗi ba fisabilillah ki auna mana ki gani.”

Cewar Rabi'ah tana yi ma ta nuni da ciwon da taji a gwiwa garin gudun ceton rai lokacin da Mahaifiyar Miemie ta sakar musu kare.

Haleema zatayi magana Suhaima da bata saka musu baki a firan ba ta riga ta da faɗin.

“amma ai koma mene ne ya faru bai kamata ki huce haushi a kan ita Miemie ɗin ba tun da ba ita ce ta sakar muku karen ba”

“Oops! Su jaɓa an sako baki bara muyi gummm...”
Rabi'ah ta yi saurin katse Suhaima da faɗin hakan tana wani juyo ma ta ƙeya. Takaici ya cika Suhaima tana shirin magana Haleema ta riga da. “dan Allah kiyi haƙuri Suhaima ke kuma Rabi'ah mene ne haka Please ki bari mana ai gaskiya ta faɗa.”

Duk shiru suka yi ma ta ba wacce ta kulata Haleema ta girgiza kai don ta rasa me ya sa sam babu ga maciji Tsakanin Rabi'ah da Suhaima duk da kasancewar yau ne suka fara haɗu wa ita Rabi'ah da ɗan banzan Surutu ga faɗi ba'a tambaye ki kuma sannan bata barin kota kwana yayin da Suhaima ta kasance miskila lamba ɗaya kuma bata shiga harkar kowa, shi ya sa Rabi'ah takeyi ma ta kallon mai shegen jijjida kai ga kuma iya yi dan kawai ta kasance ƴar minista. Dukkansu su biyun ƙawayen Haleema ne na makaranta ita Rabi'ah Secondary School suka yi tare da Haleema yayin da ita kuma Suhaima sun haɗu ne a koleji, kuma dukkanninsu suna mutunci sosai da Haleema shi ya sa a halin yanzu da lokacin bikinta ya yi suka zo ma ta sai dai sam babu jituwa a tsakaninsu hakan kuma baya yi ma Haleema daɗi dan batason ta kare ɗaya, ɗayan kuma taji haushi dan dukkansu tana ji da su a cikin ƙawayen nata.

*

“Ma sha Allah Alhamdullilah Allah ya yi mun ƙari so Wagga gari domin muyi tirirrishi kuma mu ‘YAN TIRIRRISHI nan gani nan bari kuma komai baƙin cikin Mutum dole mu ragargaji kaji!!!”

Rabi'ah ta ƙare maganar tana durowa daga Motar domin Motar nasu da suka taho cikinta irin wannan Motar ce ta ɗibar shanu to a cikinta suka taho.

Su dai sauran ƴan Matan ma dariya Rabi'ah ta basu dan sun fahimci habaici take yi ma Miemie. Yayin da Haleema ta girgiza kai kurum tasan halin Rabi'ah zatayi ma abin da ya fi hakan.

“Sannunku da ƙoƙari kuzo mu ƙari sa ciki.”

Cewar Haleema tana murmushi. Rabi'ah da ta juya baya tana ƙare ma garin kallo da gaba ɗaya bai fi ta ƙirga yawan gine-ginen ciki ba acewarta ta juyo tana ya mutsa fuska tare da buɗe baki zatayi magana daidai lokacin kuma ‘Yar Gwal ta fito daga cikin gidansu a guje hannunta riƙe da kwalla mai ɗauke da manja Iya Sahu ta biyota ita kuma ‘Yar Gwal da batasan da Mutum gabanta ba gadan-gadan ta nufo saitin da Rabi'ah da juyowarta ke nan take ai kuwa tun kafin Rabi'ah ta yi wani yunƙuri tuni aikin gama ya gama domin daga kwallar mai ɗauke da manjan har Manjan dake cike sama suka yi gaba ɗaya sannan da suka tashi yowa ƙasa basuyi masauki a ko'ina ba sai saman fuskar Rabi'ah Manjan gaba ɗaya ya wanke ma ta fuska sannan ya wanke farin Hijjabin jikinta yayin da sai da kwallar ta bugi goshin Rabi'ah sannan ta faɗi ƙasa, Rabi'ah bata gama tantance abin da ke wakana a duniyarta ba ita ma ‘Yar Gwal da Marmara ne ta taka ya sa ta yi wannan aika-aika ta faɗa jikin Rabi'ah ita ma ta sama nata rabon na manja sai gaba ɗayansu suka yi ƙasa ji kake tim! Sun faɗi , Rabi'ah ta saki ƙarar azaba tana dafe kwankwaso.

Yayin da su Haleema dake tsaye gefe daga masu salati sai masu ɓoye dariya domin yadda al'amarin ya wakana ba ƙaramin daurewa Mutum zai yi ba wurin ɓoye dariya. Ita kanta Miemie sai da ta dara musamman da ta kalla fuskar Rabi'ah da ta samu ta miƙe tsaye da ƙyar tana faman kiran sunan Allah dan a tunaninta ma da aljanu ta yi gamo suka yi ma ta wannan aika-aika ga goshinta da takeji tamkar baya kanta saboda raɗaɗin da yake yi ma ta sakamakon kwallar da ya bugu a kai.

Ihun da Uwani Matar Kawu Iliya da ta biyo bayansu ‘Yar Gwal kuma ta kasance ita ce mai wannan Manja ta kwala shi ne ya dawo da hankulansu kanta har ma da wasu mutanen gari masu wucewa dama sauran matan gidan domin ihun da Uwani ta kwala sai ka ɗauka mutuwa a ka yi ma ta, dan hannu ta ɗaura a kai tana ci gaba da zunduma ihu faɗi take.

“Ƴar Gwal kin kasheni, shikenan naja ma kaina dana hanaki bashin manja domin da ban hanaki bashin manja ba, ba zaki ɗauko gaba ɗaya kwallar manjan ba gashi yanzu kin min asara shikenan ɗan jarin da nake taƙamar ina sana'a da shi kin yi min sanadi, wayyo Allah ni Uwani tawa ta sameni!.”

Yadda Uwani ta ɗaura hannu a ka tana ihu tare da wannan sambatu abin zai baka dariya za kuma ta baka tausayi....

*😂😀Kayyasa! to dai kunji da yadda labarin namu ya fara.🤣 Ni dai nayi can 🏃*

* Happy New Year My Reader's*
_Cheer's to a fresh start, a new chapter, and a year full of dreams coming true🥰🎉_
1/1/2025!
Nainarh KD ✍️
07067953066 Or 08081129487.

♡💃YAN TIRIRRISHI 🐓💫

_Short Story_

# Nainarh KD
# Perfectly Pen's

https://chat.whatsapp.com/EKGtef2G0MxHyOMMUrN0bX

..02

Iya Sahu dake gefe sai faman salati take tana rarraba ido tama rasa abin faɗa dan kuwa ta san yau babu zaman lafiya tun da har a ka taɓa Uwani Matar Autanta Iliya bata ankara ba taga Uwani ta miƙe a fusace ta nufa wurin da 'Yar Gwal take da niyyar kai ma ta duka.

Sai dai kafin ta ƙari sa tuni 'Yar Gwal da ta ankara ta yi gefe tana dariyar ƙeta ta ce.

“kin yi ma kanki Uwani tun farko da na bi ki ta hanyar lallami da kin saurareni da duk haka ba bata faru ba ai...”

Ƙare maganar 'Yar Gwal ya yi daidai da haɗa ido da suka yi da Rabi'ah da tsaban takaici ya sa ta kasa magana.

Ai kuwa me 'Yar Gwal zatayi in ba dariya ba musamman ganin yadda fuskar Rabi'ah ta koma kamar mage ta yi ɓarin manja kasancewarta mai farar fata.

“Iya Sahu wai kuwa kina ganin abin da nake gani dan Allah tayani duba ji fa yadda fuskarta ta yi....”

Cikin dariya 'Yar Gwal take maganar tana nuna Rabi'ah da takeji kamar ta fasa ihu.

Ita kuwa Iya Sahu da sai lokacin ta lura da baƙin da suka yi idonta kuma ya sauka a kan Haleema da ta ƙari sa tana bawa Rabi'ah haƙuri ita ma 'Yar Gwal sai lokacin ta lura ta ita ta kuma gane ta.

“Laaa Auntyn Birni kece, yaushe kika zo ne?”

Cewar 'Yar Gwal cike da zumuɗi.

Ita kam Iya Sahu sai cewa ta yi.

“Haleema Amare saukar yaushe, ah lale marhaban ku shi go ciki, ashe har kin ƙari so”

Ba musu Haleema taja hannun Rabi'ah suka nufa gidan yayin da 'Yar Gwal da sauran 'Yan Matan suka bi bayansu.

Da shigarsu gidan kallo ya dawo kan su kasancewar gidan gida ne na gandu akwai mutane da yawa a ciki da zallar surukutan Iya Sahu ne.

“Rabi'ah Please kiyi haƙuri nasan bakiji daɗin abin da ya faru ba amm...”

“karki damu Haleema ba komai na haƙura”

Rabi'ah ta katse Haleema dake bata haƙuri, da kanta Haleema ta taimaka ma ta ta wanke jikinta da fuskarta sannan suka tare a Ɗakin Iya Sahu yayin da Haleema ta ware gefe guda ita da Iya Sahu suna tattaunawa.

Iya Sahu ta ci gaba da faɗin.

“amma Hafsatu ta bani mamaki ban taɓa zaton haka daga gare ta ba yanzu da ta hana kuyi TIRIRRISHI a gidanta saboda lalacewa shi ne kuma ta iya haɗa ku da ƴarta kuzo nan dan bata da mutunci”

Iya Sahu ta ƙare maganar cike da takaici  dan kuwa bata ji daɗin abin da ƴar nata wato mahaifiyar Miemie ta yi ba, shi ya sa lokacin da Mahaifiyar Haleema wato Hajiya Larai ta kira ta tana sanarda ita abin da ƴar uwarta Hafsatu ta yi ma Haleema ya sa Iya Sahu ta ce tun da haka ne su zo nan ƙauyen suyi, in ya so sai su kwana tun da gobe ne ɗaura aure in ya so bayan ɗaura auren sai su tafi domin a garin za'a ɗaura Auren kasancewar Mahaifinsu Haleema

Asalinsa ɗan garin ne kafin daga baya suka koma birni shi da Matarsa mahaifiyarsu Haleema da yaranta.

“karki damu Iya ai ba komai tana gudun kar a lalata ma ta gida ne...”

“wani gida, gidan banza da wofi a kan wani gida zata yi miki haka ta manta uwa ɗaya uba ɗaya suke da mahaifiyarki...”

Ita dai Haleema shiru ta yi tanaji Iya Sahu ta ci gaba da sababi dan kuwa ranta ya ɓaci sosai bisa abin da Hafsatu ta yi sai dai ta yi shiru dan kanta sannan Haleema ta bar wurin ta koma sashen Iya Sahu tana shiga Ɗakin ta hango Miemie ta takure a gefe guda, ajiyar zuciya ta sauke sannan ta ƙari sa wurin da Miemie take ta zauna kusa da ita tana ɗan murmushi ta ce.

“Miemie wani abun ne ya faru?”
Da sauri Miemie da batasan tazo wurin ba ta kalleta sai kuma ta girgiza kai murya ƙasa-ƙasa ta ce.

“ba abin da ya faru kawai banji daɗin Abin da Mommy ta yi muku ba ne kuma har ta iya haɗa ni daku muzo shi ya sa na kasa sakin jikina, Dan Allah Aunty Haleema kiyi haƙuri da halin Mommy muma kanmu yaranta ba raga mana take ba.”

Miemie ta ƙare maganar murya a raunace.

“karki damu kinji domin ban yi fushi ba na kuma yi ma ta uzuri, kedai ki saki jikinki ki kuma shiga mutane in ba so kike Rabi'ah ta ci gaba da tonarki ba”

Haleema ta ƙare maganar tana kallon Rabi'ah da shigowarta Ɗakin ke nan daga banɗaki take.

“ai ni bani da abin faɗa Haleema nama ji da abin da ya dameni, Bama wannnan ba gaba ɗaya tun shigowarmu garin nan na lura sam babu network kuma so nake nayi kira urgency na rasa yadda zan yi...”

“wuri ɗaya ne ake samun network mai kyau a garin nan in kin yadda zan rakaki amma sai idan Auntyn Birni ta yadda na shiga cikinku 'YAN TIRIRRISHI nima a yi dani.”

Gaba ɗaya juyawa suka yi suna kallon 'Yar Gwal dake bakin ƙofar ɗakin tana wannan magana.

“lallai kam to kun dai ji Haleema da Rabi'ah shawara ya rage naku mu dai 'yan kallo ne.”

Cewar Zieey tana dariya.

Rabi'ah ta ɗan ja tsaki tana faɗin.

“ai kuwa zaki bushe indai sai kin shigo cikinmu ne zaki kaini inda zan sama network mai kyau....”

____

Kwana biyu zaku jini shiru ban jin daɗi...

_____

Nainarh KD....

________

MARUBUCIYAR;

1. SARAUNIYAR KYAU, 1,2,3. 700₦
2. TSANTSAR SO 400₦
3. ANEESERH 500₦
4. KIN CUCENI 300₦
5. BA TABBAS 500₦
6. CAPTAIN AYUSHERH 500₦

♡‘YAN TIRIRRISHI!♡
(A Zombie story.....👽💥❤️)
2025✔️

Free Book🤗
Posting kullum amma ban da asabar da Lahadi!
Lokacin posting, da dare.

https://chat.whatsapp.com/ICXo7IragdJBkz13G5ex9G

....Masu tambayar mene ne ma'anar kalmar ‘YAN TIRIRRISHI? Ma'anar dai shi ne a taƙaice kamar a ce ƙawayen Amarya!

____

♡♡♡♡

*_Tafiya suka yi mai nisa daga wuraren da suke duk domin taya ƙawarsu murnar aurenta shi ya sa suka yarda suka yi kasadar biyota wannan wuri da sunan su ɗin ‘YAN TIRIRRISHI ne sai dai kwatsam ba tare da sanin dalili ko mafara ba sun tsinci kansu cikin wata iriyar duniya mai cike da abin tsoro yayin da wata mummunar cuta ta yaɗu ba wai cuta ba ce da a ke samu ta numfashi ko iska ko wani abu makarancin haka wannan daban ne wasu irin halitta ne na matattun mutane da suke komawa ZOMBIE da sun cije Mutum cikin lokaci ƙanƙani komai nashi

yake sauyawa shima ya koma ZOMBIE. Ta ya kuke tunanin za su iya kuɓuta daga wannan masifa? Wai ma mene ne mafarar wannan masifar ne?
Ku biyo alƙalamin NainarhKD domin warware zare da a bawa._*🤍

©Nainarh KD

...3&4

Juyawa 'Yar Gwal ta yi zata bar wurin jin abin da Rabi'ah ta faɗa.

Ganin da gaske tafiyar zatayi kuma a uzurce Rabi'ah take da ta yi wayar ya sa ta ce.

“to ina kuma zakije muna magana bamu gama ba?”

Ba tare da 'Yar Gwal ta juyo ba ta ce, “kedai ba kince baki buƙatar taimakona ba...”

“dawo Please ki kaini na yarda zaki shiga cikin mu shikenan?”

Ƴar Gwal tana dariya ta ce.

“Sosai kuwa.”

Mayafi Rabi'ah ta saka yayin da Ƴar Gwal take sanye da Hijjab da bai wuce iya gwiwa ba suna shirin fita daga Ɗakin ita ma Suhaima ta miƙe tare da furta.

“Nima zani.”

Ba tare da jira amsawarsu ba ta fice.

“Oh da gaske!”

Rabi'ah da bakinta ba ya shiru ta faɗa tana mai bin ta da wani kallo.

A tare suka fito daga gidan bayan Ƴar Gwal ta yi ma Iya Sahu bayanin wurin da za su je.

Tafiya suka yi mai ɗan nisa amma Ƴar Gwal bata ce an iso ba.

“wai kuwa nace ina zaki kaimu naga sai tafiya muke amma baki ce an kusa ba”

Cewar Rabi'ah dariya Ƴar Gwal ta yi.

“Ai sai mun yi tafiya ta aƙalla kilomita 1 sannan zamu isa yanzu kuma nasan mun yi rabi?”

“Kilomita ɗaya fa?”

“Rabi fa kikace?”

Rabi'ah da Suhaima kowacce ta jefa wa Ƴar Gwal nata tambayar tana zaro ido.

“Eh sosai ma”

“Hmmm bani labari mana akan wannan ƙauyen naku”

“Ai ke kike ganinsa Matsayin ƙauye amma ya mafi wasu state ɗin a wurin mu kawai wurin da muke rayuwa ne za'a kira da ƙauye amma inda zan kaiku yanzu ku kanku shaku sha mamaki.”

Ƴar Gwal ta bawa Rabi'ah da ta yi maganar amsa.

Jinjina kai Rabi'ah ta yi tana kuma ɗan taɓe baki alamar dai bata gamsu ba sai kuma ta ce.

“koma mene ne zamu gani”

“Sosai kuwa. Wai Amma mana na tambayeku me ya sa naga kunzo a wancan dagargajajjiyar motar bayan kuma daga birni kuke?”

Rabi'ah ta ɗan keɓe baki tana faɗin.

“Ke dai bari ai lalacewa motocin namu suka yi kamar haɗin baki shi ya sa muka hau wannan domin suma sun ce nan ƙauyen za su ƙari so shi ne suka rage mana hanya.”

Ƴar Gwal ta jinjina kai cike da gamsuwa dan Akwai taɗi kuma da alama an haɗu ne da an dace ita ma Rabi'ah ba baya ba.

Ƴar Gwal ta sake faɗin.

“To nifa har yanzu Ban san sunanku ba? Koda yake ke zan iya kiranki da Auntyn Manja dan

kuwa bakiga yadda kikayi kyau ba ɗazu da manja ya zube miki."

Ƴar Gwal ta ƙare maganar tana gimtse dariya.

"hmm ai kiyi dariya da kyau ƴar nan lokacin ki ne, ni dai Rabi'ah nake wannan kuma gata nan ki tambaye ta."

Ta ƙare tana yi ma ta nuni da Suhaima da tana jin duk firar da suke amma bata saka musu baki ba.

Tun kafin Ƴar Gwal ta ce wani abu Suhaima ta ce.

"Suhaima!"

"Suna mai daɗi."

Ci gaba da tafiyar suka yi suna ɗan taɓa fira har suka ƙara tafiya mai ɗan nisa sannan suka isa wurin da Ƴar Gwal take faɗa musu haƙiƙa ganin wurin ma ya fi jin labarin sa domin idan ka shiga ciki kamar a ce wani Garden ne ko wurin shaƙa tawa na musamman da yake ɗauke da mutane mabanbanta da zallarsu masu yawon buɗe ido ne ƙaton girma na ban mamaki wurin yake da shi, ga ɓangarori da dama har da gidan zoo shopping mall ne babu dai abin da babu Rabi'ah da Suhaima sai sakin baki suka yi suna kallon kyau girma da ƙayatuwar wurin.

"Woww amma fa wurin nan ya yi amma da wani suna a ke kiran Wurin dan nasan ba zai rasa wani suna da a ka saka masa ba"

Cewar Rabi'ah ita kuwa Suhaima sai cewa ta yi.

"Ma sha Allah amma wurin ya tafi dani I love it, can kuma ina ne nake hangowa kamar Lab na bincike?"

Ƴar Gwal tana dariya cike da murnar yabon da suke yi ma wurin ta ce.

"Ai wannan ma kaɗan kuka gani sunan wurin yana da yawa wasu na kiransa da Kasuwar Zamani wasu kuma su ce New World sai dai an fi saninsa da New World ɗin musamman masu zuwa yawon buɗe ido wancan kuma Lab ne da yake mallakin wani Bature ko mene ne ma sunan Lab ɗin...."

“Scientific Research Lab!”

Rabi'ah da Suhaima suka karanta sunan dake jikin ƙaton allon dake kafe saman dogon ginin na Lab ɗin.

“Eh tabbas haka ne kuwa. Yawwa tohm anan zaku sama network mai kyau da ƙarfi sai kuyi wayar da zakuyi.”

Cewar Ƴar Gwal.

Gyara Tsayuwarta Rabi'ah ta yi tana fuskantar Ƴar Gwal ta ce.

“Har yanzu yana biye damu ko?”

Tambayar da ta yi ya sa Suhaima da ta ciro wayarta tana ɗan latsawa ta dubeta da mamaki. Ita kuwa Ƴar Gwal da dabara ta ɗan leƙa ta bayan Rabi'ah hakan ya sa Suhaima kallon wurin da take duba.

“Eh amma ya juya baya, wai dama mu yake bi tun ɗazu fa na lura da shi.”

Ƴar Gwal ta faɗa tana dariya.

Ta ƙara da faɗin.

“Kin san shi ne Aunty Rabi'ah?”

Rabi'ah bata amsa ma ta ba sai juyawa da ta yi tare da furta.

“ina zuwa”

Sannan ta ƙari sa wurin Matashin da ya ɗan juya baya ai kuwa juyowar da zai yi sai ganin ta ya yi a gabansa. Huci ya fitar domin bai yi tazo ba dan ma namijin gaske ne shi ya sa bai nuna alamun tsoro ba.

“Wato nan ɗin ma sai da ta saka ka biyoni ko?”

“Hmmm ai kya bari na ja iska da kyau so kike zuciyata ta buga to da na firgita fa?”

Ya faɗa yana ƙoƙarin ba garar da maganarta.

“Hey Uncle!”

Ta faɗa da ƙarfi da ƙoƙarin danne ɓacin ranta.

“What!?”

Shima ya faɗa yana dubanta da fusatattun idanunsa.

Ajiyar zuciya ta ɗan sauke tana sassauta murya ta ce.

“Uncle Habib Please kar muyi haka da kai Fisabilillah a ce nan ɗin ma ba za'a barni na sha iska ba sai da ta saka ka biyoni?”

“Ki nutsu Rabi'ah ba nazo nan domin takura miki ba ne i will patiently wait until zuwa gobe da zaku yi kuma ku gama abin da ya kawo ku sannan mu juya zuwa Lagos amma idan kika bini a yadda naso ke nan a ka sin haka kuma ko kin so ko kin ƙi ta ƙarfin tsiya kuma yanzu zan koma dake Lagos kije ki zana jarabawar da kika gudo domin ta”

Shiru Rabi'ah ta yi tana ɗan cizon Lips ɗin ta. Sai kuma ta juya tana duban su Ƴar Gwal da hankalinsu yake kanta sai ta sake mayar da dubanta kansa ta ce.

“Yanzu ya kake so a yi?”

Ta faɗa rai a ɓace.

“Ko ke fa Good Girl yanzu kika dawo kan hanya. Yanzu dai kije ga ƴan uwan tafiyarki suna jiran ki kuma wannan tafiyar da kuka yi a ƙasa ta yi nisa su zo na mayar da ku a mota.”

Bata ce masa komai ba ta juya zuwa wurinsu Ƴar Gwal.

Da Dare!

“Aunty Rabi'ah wai wanene mutumin ɗazu ne kin san kuwa har yanzu yana nan cikin Anguwan ya Parker Motarsa yana ciki amma fa kyakkyawa ne hala saurayinki ne?”

Ƴar Gwal ta ƙare maganar cikin raɗa raɗa tana duban Rabi'ah da ta yi nisa da danna waya.

Shiru Rabi'ah ta ɗan yi tana tuna yadda suka kwashe ɗazu shi ne ya dawo da su ba tare da ta yi wayar da ta yi niyya ba dama taso ta kira Mahafiyarta ne ta sanar da ita da kar ma ta damu in taga bata nan kuma tana a Safe Place sai dai ganinsa da ta yi ya sa ta fasa dan tasan za'ayi haka.

“Kyaleshi kinji idan ya gaji zai tafi”

Ta faɗa ba tare da ta dubi Ƴar Gwal ɗin ba.

Ya mutsa fuska Ƴar Gwal ta yi dan ba haka taso ji ba sai ta ƙara faɗin.

“To baki ce saurayinki ba ne hala dai saurayin naki ne?”

Wannan karon dubanta Rabi'ah ta yi tana sauke numfashi ta ce.

“Ƴar Gwal right? What's your Intention hmmph? to ba saurayina ba ne Uncle ɗina ne”

Bata rufe baki ba taga Ƴar Gwal ta yi wani zaman daɓas tana ɗaura tafin hannunta saman fuskarta irin maganar ba ƙaramin daɗi ya yi ma ta ba.

“And kar ma ki yi wani tunani daban.”

“Saboda me Aunty Rabi'a's?”

Ƴar Gwal ta tambaya tana wani zaro ido. Har da wani lauya ma ta suna zuwa Rabi'a's.

“Saboda shi ɗin Soja ne”

Maganar da ta yi ya sa Ƴar Gwal zaro ido tare da kwanciya ba shiri tana rufe ko'ina na jikinta sannan ta duba Rabi'ah ta ce.

“Sai da safe!”

Maganarta da kuma reaction ɗinta ba ƙaramin dariya ya bawa Rabi'ah ba.

Hakan ya sa ta dara tana ɗan girgiza kai dama su biyu suka rage basu kwanta ba hakan ya sa ita ma ta yi kwanciyarta.

WASHEGARI!

Kasancewar da wuri motocin guda biyu da suka lalace musu a jiya suka ƙari so kuma da yake duk wani abu da za su amfani da shi yana ciki shi ya sa sai da suka jira ƙari sowar Motocin suka kawo musu kayan sannan zuwa sha ɗaya na safe suka fara aiki ka'indana'in abinci suka girka kala-kala lafiyayyu na gani na faɗa gidan sai ƙamshi ke tashi da yake ɓangare guda a ka basu kuma anan suka kwana jiya wato ɓangaren Uwani Matar Kawu Iliya da yake baya nan ita kuma Uwani taga ƴan birni da gayunsa ga turanci ita kuma a Duniya abun da yake burgeta shi ne ta ganta gata ga ƴan birni ko ɗan gayu musamman a ce yana turanci shi ya sa jiki na rawa ta basu ɓangarenta suyi abin da suke so ita sai a Ɗakin Iya Sahu ta kwana da yake ma bata taɓa haihuwa ba dan ko shekara basu yi da aure ba dan ma Kawu Iliya ɗin ba mazauni ba ne kuma shi ne kaɗai namiji cikin ƴaƴan Iya Sahu dama yaranta uku kacal mahaifiyar Haleema ita ce Babba sai kuma Mahaifiyar Miemie sannan sai Auta Iliya dukkansu a Abuja suke Aure sai dai duk yadda Mahaifiyar Haleema taso shawo kanta a kan ta koma Abuja wurinsu ƙi ta yi shima kuma Iliya da yake ba wani damunsa zama a birnin ya yi ba shi ya sa duk da a can ya taso hannun Mahaifiyar Haleema amma sai ya yo gudowarsa ya yi aure anan ƙauye duk da ba haka Mahafiyar Haleema ta so ba.

Wani irin ƙamshin suyan kaji ne da ya cika gaba ɗaya gidan ya sa ba shiri Uwani dake tsakar gida suna fira da ɗaya daga cikin surukan Abokiyar zaman Iya Sahu ba shiri ta tashi tare da nufar ɓangaren nata garin sauri har tana kusan tuntuɓe sai dai cak! Taja tunga lokacin da ta karya kwana ta ƙari sa ɓangaren ganin yadda suka wani baje suna cin abinci a nutse yayin da wasu ke suyar nama.

“Yawwa ga wannan ki miƙa wa Iya Sahu ta bawa kowa da kowa sai ki dawo ki shiga da wannan Ɗakin Aunty Uwani ki a je wanda zamu wuce ma su Mommy da shi ne ai haka kika ce ake yi ko?”

Suhaima da Haleema ta bar ma ta ragamar komai ta ƙare maganar tana duban Ƴar Gwal dake

siɗe hannu dan kammala cin Jallof ɗin Spaghetti da ta yi ke nan washe baki ta yi dama kuma ita ce take faɗa musu duk abin da a ke yi domin Dukansu har Haleeman ba wacce ta san ya ake wani Tirirrishi sunan ma sai a bakin Iya Sahu Haleema taji shi ne tun da ta kira su da shi ita kuma Rabi'ah ta kama, Haleema duk da ta kasance wayayyiya kuma wacce ta yi ilimi mai zufi amma tana son yin abubuwa na al'adar Malam bahaushe muddun bai saɓawa addini ba shi ya sa sai da tasan yadda ta yi a ka zo yin wannan Tirirrishi ita hana su zama a gidanta da Mahaifiyar Miemie ta yi ma daɗi ya yi ma ta dan dama tafiso suyi a ƙauyen kuma anan ɗin sun fi sakin jiki duk da tafiyar mai nisa sukayi.

Karɓan kulolin ta yi bayan ta bawa Suhaima amsa sannan ta tafi ta kai da ta dawo ta tarar da Rabi'ah tana raba halin dan ba'a ce da kowa take ba sai dai in ta yi wani abun kawai Suhaima ko Miemie da ta fi sakawa ido su yi murmushi dan ta dena basu haushi sai dariya dan sun lura ita haka take.

Wani abincin mai yawan gaske Suhaima ta sake bawa Ƴar Gwal ta ce a kaima Uwani ai kuwa farin ciki da murna kamar me a wurin Uwani musamman ganin uban naman dake ciki kuma duk da wurin kala huɗu suka yi abincin amma sai da suka ɗiba ma ta a ko wanne kaɗan ta ɗiba ta adana sauran tana faɗin sai Mijinta Iliya ya dawo da yake sun yi waya ya sanar da ita yana hanya, ita Uwani bawai nama ne bata taɓa ci ba a'a tsaban ɗoki ne kawai da yadda ƴan gayu da komai nasu yake burgeta shi ya sa ma yanzu jiki na rawa take cin abincin na ‘YAN TIRIRRISHI saboda sun kasance ƴan gayu.

Zuwa bayan wani lokaci ma tuni sun fara shiga wanka suna shirye-shiryen ɗaukar hanyar komawa Abuja da yake da Iya Sahu da kuma Uwani har da Ƴar Gwal za'a je shi ya sa dukkansu shiri suke ba kama hannun yaro musamman ma Uwani da Ƴar Gwal da suka fi kowa zaƙuwa da ƙosawa wani abun ma idan suka yi sai dai su Haleema suka yi ta dariya cikin nishaɗi suke gabatar da komai har zuwa wani lokaci da suka ji garin ya ɗauki wani irin hayaniya kamar me can kuma iface-ifacen mutane ya biyo baya kafin wasu mintuna sai ga Habib ya shigo a wani irin jigace cikin sa'a kuwa ya hango Rabi'ah da duk sun gama shirya wa sai dai suna tsaye ne cirko-cirko cikin rashin abin yi domin wannan hayaniya da iface-ifacen bana lafiya ba su sun ma yi tunanin ko ƴan fashi ne.

“Rabi'ah taho mu bar Garin nan da sauri babu lafiya...”

“Wai mene ne yake faruwa Uhum Uncle Habib ko dai Ƴan fashi ne?”

Rabi'ah ta tambaya a ruɗe tana ƙoƙarin kwace hannunta da ya riƙe ƙam. Su kam sauran jin ta ambaci ƴan fashi duk da suma haka suke zargi amma hankalinsu ba ƙaramin ƙara tashi ya yi

ba.

“Ba lokacin da zan yi miki bayani ba ne yanzu kizo muje kawai kuma kwara ma a ce ƴan fashi ne suka kawo farmaki bisa abin da yake faruwa....”

Maganar Habib ya maƙale a fatar bakinsa lokacin wasu suka shigo gidan a guje su biyu ne sai kuma wani halitta da suka rasa gane kansa da ya buga wani uban tsalle ya cafki wuyar ɗaya daga cikin mazan da suka shigo a guje ya danne shi a ƙasa yana wani hargagi lokaci guda kuma yana ta ƙoƙarin cizonsa duk yadda mutumin ya so kare kansa lamarin ya cutara sai da wannan abu ya cije shi a wuya kuma a take ya fito da naman wurin da hakan ya ƙara jefasu cikin tashin hankali har da masu yunƙurin amai domin lamarin ba kyan gani.

“M..m.. mene ne wannan Uncle...?”

Rabi'ah ta faɗa idanunta suna rufe wa alamar dai suma za ta yi. Hankali tashe Habib ya juya yana jijjigata tare da kiran sunanta sai dai ko motsi bata yi kuma a daidai wannan lokaci wannan halittar ya miƙe tsaye tare da nufar Habib da gudun gaske domin aiwatar da ƙudirin ruhinsa a kan sa wato da ya ci namansa domin a wannan taƙin da yake wata iriyar balaƴa'iyar yunwa ce ke damunsa da yake ji in ba naman bil'adama yaci ba to fa babu zaman lafiya kamar kuma ba naman mutumin da ya ciza bane a bakinsa bai gama ci ba...
Rashin comments kan iya sa na dakata da posting gaba ɗaya.🤗
NainarhKDnkd's
07067953066

♡‘YAN TIRIRRISHI♡

P. 5,6,7

...©NainarhKDnkd's

“Zo...zo..zombie?!”
Wata daga cikin ƙawayen Haleema ɗin mai suna Mary ta faɗa a rikice.
Daidai lokacin ita kuma Ƴar Gwal da taga yadda wannan abu ya tunkaro Habib ta ware murya tare da faɗin.
“Ka kula gashi nan ya tunkaro ka!”
Su kuwa sauran jama'ar wurin jin abin da Mary ta ce ne ya sa waɗan da suka gane abin da take nufi cikin tsananin ruɗe wa har suna haɗa baki wurin faɗin.
“Zom... Me?!”
Tuni wasu sun fara guduwa ɗakuna suna ɓuya dan wannan bala'in da suke gani ido biyu sun yi zaton wata ƙila mafarki ne zuwa anjima za su farka duk dai ba sun gana fahimtar abin da yake faruwa ba ne.

Da wani irin mugun sauri Habib ya juya lokacin da yaji abin da Ƴar Gwal ta ce sai dai cikin rashin sa'a juyawar da zai yi hakan ya yi daidai da kai masa farmaki da abin ya yi cikin jarunta ya yi saurin tarewa sai dai da yake shammatarsa abin ya yi kuma wani mugun ƙarfi na ban mamaki ne ya sa shi rinjayar Habib suka faɗi a tare yana ci gaba da ƙoƙarin ya kai ma Habib farmaki burinsa kawai ya cije shi kuma duk yadda Habib ya yi ƙoƙari wurin ganin ya cececi kansa abu ya cutura Zombie'n yana daf da kai masa cizo ke nan sai kwaf! Suka ji ƙarar buga abu mai ƙarfi da a ka yi a kan Zombie'n da yake da mugun ƙarfi a ka buga nan take kuwa kan nasa ya fashe jini ya fara wani malala da sauri Habib ya mirgina da Zombie'n gefe sannan ya miƙe yana sauke haki tare da mayar da dubansa kan Ƴar Gwal dake riƙe da ƙaton gatarin da ta buga a kan Zombie'n har ya fasa kansa jikinta babu inda baya rawa sai zare ido takeyi sai kuma lokaci ɗaya ta yi wurgi da gatarin tare da kurma ihu taja gefe tana sauke haki idanunta a kan Zombie'n da ko motsi bayayi.

“Uncle Habib wai mene ne wannan kamar abin nan da nake gani a Film ne yake faruwa ido biyo yau a gabana na shiga uku na, Dan Allah kucemin mafarki nake ba zahiri bane duka abin da na gani”

Rabi'ah ta faɗa tana rumtse ido cikin tashin hankali.

“Tabbas wannan abu Zombie ne kuma ba shi kaɗai ba ne domin zuwa yanzu kusan rabi ko na ma ce fiye da rabi na mutanen garin nan sun koma Zombie's ni kaina mamakin wannan cukurkuɗaɗen al'amarin nake.”

Habib ya bata amsa yana mai dubansu gaba ɗaya.

“Amma kuma daga ina wannan masifa ta fara kuma a Nigeriya, Nigeriya ma yankin Arewa a ce an wayi gari ana zama Zombie's bayan Duniya ta tabbatar da tsabagen lafiya da baƙaƙen fata suka fi fararen fata irin wannan abu bai taɓa faruwa da baƙaƙen fata ba sai dai a jishi a yankin farare amma mene ne sila yau an wayi gari yankin baƙaƙe suna komawa Zombie's kuma dole akwai wata a ƙasa.”

Gaba ɗaya duban Suhaima da take maganar cike da al'ajabi suka yi Habib ya ce.
“Daga jin kalamanki koda ke ba likita ba ce to tabbas kin san wani abu a kan fannin lafiya sai dai yanzu ba lokacin wannan ba ne bamu da isasshen lokaci barin garin nan zamuyi tun kafin gaba ɗaya mutanen ciki su koma Zombie's....”

Maganar Habib ta katse ne lokacin suka ga wannan Mutumin na farko da a ka ciza ya yi wani

motsi lokaci guda kuma jikinsa yana wani irin ƙara da makwalkwashewa da alama shima Zombie'n zai zama.

“Ku jajja baya.”

Habib ya faɗa yana duban Mutumin.

“Jesus Christ, yeh yyeh jama'a kuna gani shi ma Zombie'n zai zama!”

Mary ta faɗa da gurɓatacciyar hausarta tana nuna Mutumin cike da tsoro.

Wani irin kuka Miemie ta fashe da shi lokaci guda kuma suna ƙanƙame juna ita da ‘Yar Gwal da ita ma hankalinta yake a mugun tashe ganin wannan tashin hankali da tun da uwarta ta haifeta bata taɓa gani ba.

“Innalillahi wayyo Allah na shiga uku na ya tashi jama'a tashi ya yi fa!”

Rabi'ah ta faɗa a matuƙar ruɗe idanu warwaje take duban wannan mutumin da ya fara motsi jikinsa yana wani irin malkwashewa ƙasusuwansa suna bada wani sauti lokaci guda fuskarsa ya koma wani irin abin tsoro ga saitin wurin da a ka cizesan ya yi wani mugun rami yana fitar da wani wawwaran jini.

“Shima fa Zombie'n ya zama wayyo Allah!”

Haleema ta sake faɗa cikin tsananin tashin hankali tana ƙamewa wuri guda ta ma kasa motsi bare tunanin gudun ceton rai.

Wani irin hautsinewa ƴaƴan cikin ‘Yar Gwal suka yi ganin mummunar halittar da Mutumin ya koma da kuma jin abin da Haleema ta faɗa rashin abin yi da kuma tashin hankali ya sa ta ɗafale bayan Miemie ba tare da ta sani ba tana sakin wani marayan kuka.

———

24HRS Back....
Awanni ashirin da huɗu baya.

*Scientific Research Lab*

Wani irin gini ne mai tsayi da girma da kuma tsari kana gani kasan turawa ne suka tsara abin su kuma daga yadda suka yi ginin zaka fahimci cewa Lab ne wato wurin bincike kuma na kimiyya duba da sunan da a ka saka ma sa.

Daga cikinsa ma yafi wajen kyau wuri ne iri-iri ɓangare-ɓangare ko wanne ma'aikata ne na kiwon lafiya masu bincike cikin uniform suna gudanar da aikinsu cikin kwarewa daga can gini na ƙarshe kuwa cikin Lab ɗin wani irin ɗaki ne mai girman gaske da ya haɗa abubuwa da dama na bincike daga can gefe guda wani Matashi ne bak'ar fata wankan tarwatsa dogo, da ba zai haure shekaru talatin da biyu ba yana tsaye sanye da Lab coat sai Goggles irin wannan Glasses ɗin da masu bincike suke sakawa a idanunsa sai kuma face mask dake fuskarsa ya juya baya hannunsa dake cikin Gloves riƙe da Lab notebook yana rubutu a hankali a ciki gaba ɗaya hankalinsa ya tattara ne ya mayar a kan wani gilashi mai girman gaske dake gabansa a tsaye gilashin yake ciki kuwa wani mutum ne kwance a ciki idanunsa a rufe, baya motsi tamkar babu rai a tare da shi ga kuma wani ruwa mai haɗe da sinadari dake a cikin gilashin ruwan mai launin shuɗi-shuɗi.

A wani irin hargitse a ka turo ƙofar wurin wani Matashin Bature da a Shekaru za su daidai da baƙin fatar dake ciki, Baturen ya bayyana yana mai sauke huci cikin ɓacin rai yake duban wanda yake cikin da ya juyo yana bin sa da kallon lafiya? Sai dai tun kafin ya ce wani abu, rai a ɓace Baturen ya fara faɗin.

“Why Sadiq me ya sa ka zaɓi wannan hanyar? me ya sa tun fari baka faɗa min gaskiya ba kayi amfani dani da Lab ɗina ka haɗa kai da wasu mutane can badan kuna shirin yaɗa ɓarna ku cutar da mutane?”

Tun da ya fara Maganar cikin harshen turanci wanda ya kira da Sadiq ɗin ne ya wani harɗe hannu a ƙirji bayan ya a je Lab notebook dake hannunsa idanunsa kafe a kansa bai katse shi ba har sai da yaga ya yi shiru dan kansa sannan ya saki wani malalacin murmushi da ya bawa abokin nasa Bature mamaki.

“Daniel Jack ke nan wa ya faɗa maka wannan Sadiq ɗin dake gabanka shi ne abokinka da ka sani shekaru masu kauri a baya? To wannan wani Sadiq ne sabo da ba abin da ya saka a gaba sai neman Duniya kuma ina dab da samu sannan da kake maganar wasu mutane can daban ai sun ɗin Turawa ne kamar ka saboda haka ka ma dena kiransu da wasu mutane can daban dan duk halin ku ɗaya ban da haka mai zai saka duk kuɗaɗenka ka baro ƙasar ka kazo nan ka buɗe wannan Research Lab ɗin?”

“Saboda ina son na taimakawa al'ummar Duniya da baiwar da nake shi a ɓangaren”

Daniel Jack ya katse shi da faɗin hakan a fusace sannan ya ci gaba.

“kuma da kake maganar su waɗan da ka haɗa kai da su kuke shirin aikata wannan ɗanyan aiki sun kasance Turawa ai ba duka ne aka taru a ka zama ɗaya ba domin ni Bature ne amma son zuciya da neman Duniya ba zai taɓa rufe min ido nayi wannan aika-aikar ba bare kuma kai daka kasance musulmi kuma a ƙasarka da danginka suke a ke ƙoƙarin wannan yaɗa ɓarna karfa ka manta zombie kuke shirin farmakar ƙasarka da shi, wai kuwa ka manta haɗarin da wannan abu yake da shi ne? Ba fa ƙasarka ba hatta Duniya ba zata tsira ba da abin da kuke shirin yi saboda haka ina roƙonka for the sake of our true friendship ka dakata da wannan abu da kake shirin yi.”

Wata ƴar iskar dariyar ƙeta da Sadiq ya saki ita ce ta sa Daniel Jack ya yi shiru jikinsa ya yi sanyi yana yi ma Sadiq ɗin wani irin duba cikin sanyin jiki bai taɓa tunanin kuɗi za su canza abokin nasa ba musamman da ya san shi da halaye nagartattu ga kuma addinin da yake ciki da a har kullum sha'awa yake bashi kuma shi ma yana da burin wata rana ya kasance cikin jama'a na wannan addini.

“A kan kuɗi kake komai ba? Me ya sa tun farko baka sameni ka sanar dani ko dala biliyan nawa kake buƙata ba amma ka zaɓi bin wannan gurɓatacciyar hanya?”

Daniel Jack ya kasa ci gaba da maganar ganin wannan gilashin da mutumin ke ciki ya fara tsagewa yayin da Mutumin ya buɗe idanunsa gaba ɗaya halittar jikinsa ya gama komawa irin na zombie sak ko kafin Sadiq ya ankara Mutumin da ya koma zombie ya fara ƙoƙarin ganin ya fasa gilashin duk kuwa da mugun ƙarfin da yake da shi.

Cikin wani irin ruɗe wa hankali a tashe Daniel Jack ya cillar da Airpad ɗin hannunsa sannan ya ƙari sa wurin da mugun sauri ya janye Sadiq daidai lokacin kuma wannan zombie ɗin ya sama nasarar fasa gilashin aikuwa cafka ɗaya ya yi ma Daniel Jack dake tsaye a wurin ya kafa masa haƙoransa irin na zombie a wuya wani irin masifafen zafi da raɗaɗi ya sa Daniel Jack ya durƙushe ƙasa duk da haka idanunsa na kan Sadiq da tun da Daniel Jack ya yi gefe da shi ya ɗan fadi sai ya tsaya ganin ikon Allah cikin tashin hankali.

Cikin wani irin dauriya na jin raɗaɗi Daniel ya furta.

“Ka gudu Abokina ka ceci kanka sannan ka yi ƙoƙari ka dawo cikin hayyacinka ka dakatar da ɓarnar da kuke shirin yaɗa wa Innocent people da yawa za su rasa rayukansu”

Shiru ya yi sakamakon ƙasusuwan jikinsa da suka fara wani irin ƙara idanunsa suna rinewa zuwa sifar na zombie take kuma jikinsa ya fara wani irin malkwashewa shi kuma yana fitar da ƙara da kuma gurnani.

Cikin kiɗima Sadiq ya tashi yana ƙoƙarin ƙari sawa wurin da Daniel yake sai dai take wannan Zombie ɗin ya fara ƙoƙarin kai masa farmaki hakan ya sa suka shiga ƴar tsere yayin da dabara Sadiq yake tattara abubuwan sa masu amfani yana sakawa cikin wata backpack sannan ya rataya a wuyansa zuwa lokacin shi ma Daniel ya gama zama zombie da wani irin masifar gudu Sadiq ya baro Room ɗin tare da datse ƙofar sai dai tun kafin ya yi nisa wannan Zombie ɗin da kuma Daniel shima da ya zama Zombie suka ɓalla ƙofar suka fito ma'aikatan wurin da basu san abin da yake faruwa ba suka fara guje-guje sai dai duk wanda Zombie's suka samu cizo suke yi zuwa wani lokaci shima kuma ya zama zombie hakan ya sa cikin ƙanƙanin lokaci ƙasa da awanni ashirin da huɗu Kasuwar Zamani ko kuma a ce New World ta zama labari domin duk jama'ar ciki sun koma zombie sai waɗan da Allah ya ba wa damar ƙubuta ƙauyuka da garuruwa dake makwabtaka da kasuwar ma tuni Zombie's sun kai musu farmaki.
WANNAN KE NAN!
CI GABAN LABARI.
More comments more more and more na posting da zaku ke samu.!

♡‘YAN TIRIRRISHI♡

...©NainarhKDnkd's

https://chat.whatsapp.com/ICXo7IragdJBkz13G5ex9G

P.8,9

Baya suka ja da sauri ganin yadda yake tunkaro su yana wani irin gurnani, alama Habib yake yi musu da suyi su bar gidan ya musu nuni da hanyar fita sai dai tsoro da tashin hankali ya sa suka kasa fahimtar abin da yake nufi dan sun kasa ma motsi, da gudu ɗaya daga cikin matan gidan ta nufa wata hanya daban bana fita ba tana kurma ihu ai kuwa shima Zombie'n ya mara ma ta baya kafin ta ankara ya cakumota sun fara ciniya yayin da ya sama nasarar cizonta a ciki ya farka wurin ya zaro ƴan hanjinta ya kai musu wawusa, wannan tashin hankalin ya sa Iya Sahu sumewa Haleema da ita ma takeji dama sumar tayi da ya fiye ma ta ta yi saurin tarota ganin zata faɗi tana kiran sunanta shi kuwa Habib hannun Rabi'ah ya damƙa bai sake bi ta kan kowa ba ya nufa waje da ita ganin haka ya sa duk suka mara masa baya cikin tashin hankali amma banda Uwani da ta tsaya ƙiƙam ta kasa gaba bare baya.

“Me kike jirane Uwani kizo muje ko kuwa so kike kema ki mutu?”

Ƴar Gwal da ta ɗan dakata ta faɗa tana duban Uwani, a hankali Uwani ta ɗa go ta duba Ƴar Gwal sai kuma kawai ta fashe da kuka tare da zaman ƴan bori a ƙasa, takaici ya sa Ƴar Gwal taji kamar ta shaƙeta, ji ta yi kamar ta tafi ta barta, sai kuma ta ƙari sa wurin Uwanin da gudu tare da damƙo hannunta Uwani ta miƙe tsaye tana share majina da hawaye sun yi taku ɗaya biyu a na ukun sai ji Ƴar Gwal ta yi Uwani ta maƙale taƙi ci gaba da tafiya.

Kallon yanzu kuma mene ne abin da kike nufi Ƴar Gwal ta yi ma Uwani sai kuwa Uwani buɗar bakinta sai cewa ta yi.
“Wayyo Allah Abincina! Abincin ‘ƳAN TIRIRRISHI”

Slowly Ƴar Gwal juya gaba ɗayanta tana bin ta da wani irin kallo na takaici sai dai kafin ta kai ga furta komai Uwani ta juya da gudu ta nufa ɓangaren ta da gudun da ta yi ne kuma ya dawo da hankalin wannan zombie ɗin kanta daidai kuma lokacin Ƴar Gwal ta mara ma ta baya da yake ta saitin zombie ɗin ne sam bata lura da yadda hankalinsa ya dawo kansu ba.

“Na rantse da Allah idan baki fito ba zan tafi wato ke ana gari ba lafiya ke kuma ta abinci kike.”

Ƴar Gwal da ta tsaya a tsakiyar ɓangaren Uwani ta faɗa hakan cikin ƙosawa daidai lokacin kuma Uwani ta fito kinkime da kuloli har biyu ta buɗe baki zata yi magana idanunta suka yi kyakkyawan ganin da ya sa ba shiri kula ɗaya dake hannunta ta suɓuce ta yi ƙasa ita kuma ta saki baki so take ta kwala ihu ko a kawo ma ta agaji amma ta kasa bare har ta ankarar da Ƴar Gwal abin da ta gani, ganin yadda Uwanin ta yi ne ta kuma kafe gefe guda da kallo ya sa Ƴar Gwal juyawa domin ganin abin da Uwanin ke kalla da ya sa ta kafe wuri guda kamar wata Status.

Ai kuwa idanunta suka yi ma ta karo da wannan zombie da yake tunkaro ta cikin wani irin tafiya yana jan ƙafa sakamakon hannun bokitin ƙarfe da ya maƙale masa a ƙafan tashin hankali da ruɗani ya sa Ƴar Gwal ta rasa abin yi sai kawai ta rimtse idanunta da ƙarfi ganin yadda ya wani tunkaro ta yana buɗe bakinsa dake malalar jini ga fuskar nan tasa gunin ban tsoro da tashin hankali.

Shiru ta yi tana jiran mai afkuwa tana jiran taji an damƙi wuyanta ana yagan naman amma jin shiru ba abin da ya faru ya sa slowly ta fara buɗe idanunta sai kuwa ta ware su kan Habib dake kokawa da Zombie da sauri ta ƙara ware idanunta cike da mamaki a zuciyarta ta ce. “Shi wannan ko tsoron wannan mugun abu ya cije sa shima ya zama irinsa baya yi?”

Cikin Sa'a Habib ya sama nasarar tura Zombie'n cikin wani ɗaki dake ɓangaren da ba komai sannan ya maza ya rufo ƙofar, dubansu ya yi yana sauke haki.

“Ku tafi..”

Ai tun kafin ya rufe baki Uwani ta yi gaba ko ta kan kularta guda ɗaya da ta faɗi bata bi ba, ita kuwa Ƴar Gwal tsaban neman magana sai da ta ƙari sa ta ɗauki kular abincin da Uwani ta ƴar sannan ta bi bayanta sai da Habib ya tabbatar da sun yi nisa sannan ya mara musu baya.

Da yake lokacin da suka fita har sun shiga mota Rabi'ah ta ankara da Ƴar Gwal bata fito ba shi

ne ta roƙi Habib da ya dawo ya taho da su shi ne ya dawo.

Cikin motar Habib da Rabi'ah ke zaune gaban motar Ƴar Gwal da Uwani suka shige yayin da shi kuma ya shiga mazaunin driver sauran Motocin guda biyu kuma na 'ƳAN TIRIRRISHI shi su Haleema suka shiga Allah ya taimake su Direbobin suna nan.

Da wani irin gudun tsiya suka ja motocin domin barin ƙauyen sai dai kuma me? Babu hanya domin rabi da rabi na mutanen ƙauyen sun zama Zombie's kuma wurare da dama wuta ke kamawa a ƙauyen shi ya sa gaba ɗaya hanya ta toshe sun kasa samun hanya ga kuma yadda Zombie's ɗin suke ta uban kai ma musu farmaki da yake motar Habib ne a gaba shi ya sa ya kusa yabi da su ta cikin daji cikin tsula gudu sauran motocin na take masa baya.

*Abuja, Nigeria.*

Tun waye war garin yau ta lura da ita sam bata cikin nutsuwarta kuma da an tambaye ta sai ta ce ba komai shi ya sa ta bari sai da suka bar cikin mutane kasancewar gidan maƙil yake da ƴan biki sakamakon yau ɗaura aure, bayan an ɗaura auren Wuraren uku na yamma ta sameta a bedroom ta zauna shiru da alama ta yi nisa ne a Duniyar tunani.

“Mama! Mama”

Ta kira sunanta sai dai shiru hakan ya sa ta ɗan taɓe ta tana ci gaba da kiran sunanta firgita ta yi sai kuma ta dubeta tana ƴar dariya ta ce.

“Ah Hafsa kece? Yaushe kika shigo ban sani ba?”

Bata ce mata komai ba sai da ta zauna gefen gadon suna fuskantar juna sannan ta dubeta cikin kulawa ta ce.

“Mama ba tun yau ba tun jiya nake lura kamar wani abu yana damunki kamar kina cikin damuna amma da an tambaye ki sai ki ce babu komai bayan kuma da komai ɗin ko dai abin da Mommyn Miemie ta yi ma Aunty Haleema da ƙawayenta ne ya sa kike damun kanki har haka?”

Girgiza kai Mama ta yi sannan ta ce.

“Da wannan dan wannan amma a sanin halin Zuwaira (Mahafiyar Miemie) da nayi zata aikata fiye da hakan shi ya sa ban damu ba ko kaɗan duk da abin da ta yi ya yi min zafi sosai saboda ita ɗin ƴar uwata ce ɗaya kwallin kwal da nake da amma ta biye son zuciya.”

Cike da takaici Hafsa ta girgiza kai ta ce.

“Ai Mama indai Mommy Zuwaira ce zata yi abin da ya fi haka ba gashi ba saboda tsaban rashin ta ido bayan tayi ma su Haleema wannan tsiyar kuma har da wani iya haɗa su da ƴarta, dama fa baƙin ciki kawai take yi saboda Haleema zata aura wanda ya fi mijin da ƴar ta take Aure komai na rayuwa kama daga kuɗi nasaba da kuma kyawawan halaye....”

“To ai shikenan ai ta yi ma kanta ni yanzu abin da yake ɗa ga min hankali wannan doguwar tafiya da su Haleema suka yi zuwa ƙauye tun da suka tafi hankali na ba'a kwance yake ba sam wani irin faɗuwar gaba nake ji dana rasa dalili gashi tun safe nake gwada kiran layin Haleema amma bata shiga.”

Mama ta katse Hafsa da faɗin hakan cikin yanayi na damuwa.

♡'YAN TIRIRRISHI♡

...©NainarhKDnkd's

https://chat.whatsapp.com/ICXo7IragdJBkz13G5ex9G

P.10,11.

“Karki damu in sha Allahu ma babu abin da yake faruwa sai Alkhairi kin manta can ɗin ana iya samun matsalar network ne?”

Cewar Hafsa ta faɗa hakan ne ba dan komai ba sai dan kwantar ma da Mahafiyar nata hankali duk da ita ma tana cikin damuwa domin tun bayan ɗaura auren ango da kansa ya kirata yana yi ma ta ƙorafin tun safe da suka yi waya da Haleema bai sake samun layinta ba shi ya sa hankalinsa ya kasa kwanciya, lokacin da yake faɗa ma ta haka ba ƙaramin tashin hankali ta shiga ba sai dai ta daure tare da faɗa masa ya kwantar da hankali ba wani abu wata ƙila matsalar network ne da haka ta rabu da shi sai dai ganin an kawo i yanzu ba wani labari ita ma hankalinta ya tashi sosai musamman da ya kasance ba'a samun layin kowa hatta shi ma Uncle Iliya da bayan ɗaura aure ya kama hanyar komawa ƙauyen, daurewa kawai ta yi ta hanyar ci gaba da kwantar ma da Mama hankali da tausasan kalamai na kuma tabbatar ma ta sa in sha Allah ba abin da yake faruwa da haka ta samu ta bar bedroom ɗin.
*****
Tafiya suka yi mai ɗan nisa kafin motar Habib ta maƙale wuri ɗaya duk yadda ya so ta ci gaba tafiya abu ya cutura gashi cikin daji suke kuma yamma ta fara sako kai a dole duk suka fito daga motocin ganin nasa ya tsaya yayin da ya je yana duba matsalar dake damun motar su kuma suna tsay-tsaye cirko-cirko cikin rashin madafa Iya Sahu lokaci-lokaci take share hawaye da an tambayeta sai taƙi kula kowa can kuma sai cewa ta yi.
“Allah Sarki Tasalla (Abokiyar zamanta) ko wani hali take ciki yanzu ita da surukanta oho.”

Sai suka ga Iya Sahu ta saka kuka har da wani sheshsheƙa.
Duk shiru suka yi dan sun ma rasa abin faɗa sai Haleema ce ta sama zarafin faɗin.
“Kiyi haƙuri Iya Sahu in sha Allahu ba abin da ya samesu kamar yadda muka gudu suma za su sama wurin ɓuya...”
“Wani na yi haƙuri ƴar nan kina dai gani a gabanmu wancan mugun halittar Zommie ko me kukace sunanshi ya cije ɗaya daga cikin surukan Tasalla, shikenan ita ma nasan zuwa yanzu ta zama kamar sa ni dai ba zan gaji da faɗin Allah ya kwashewa waɗan da suka ƙirƙiro wannan masifa albarka ba shikenan ƙarshen duniya tazo.”

Iya sahu ta sake fashewa da kuka bayan ta kai nan a zarcenta abin nata ya basu dariya da kuma tausayi haka dai Haleema ta ci gaba da rarrashi.

“Yanzu ya zamuyi ke nan ba zai yiwu mu ci gaba da tsayawa anan na tsawon lokaci ba saboda Akwai matukar haɗari yin hakan gashi kuma dare na kawo kai motar taka kuma taƙi yi...”

“Haba Muhsin wani irin magana kake haka au wai kai da a tunaninka ci gaba da tsayawa zamuyi a nan wallahi ba zata saɓu ba idan kaga zaka iya Allah ba mai rabo Sa'a ni dai kaga tafiya ta kawai ina ji ina gani ba zan bari na kashe kaina a banza ba.”

Ɗayan Drivern ya katse ɗayan da ya fara magana yana maganar bai ma sake bi ta kan wanda ya kira da Muhsin ɗin ba ya shige mota yaja da gudu ya bar dajin ya ƙara gaba duk irin kiran da Muhsin ɗin da su Haleema suke kwala masa yaƙi tsayawa ai kuwa ko dena hangosa basu yi ba kamar ance Mary ta duba gefenta kwatsam taga Zombie's har guda uku suna tahowa ɗaya ma babu hannnaye da ƙafa ɗaya a tare da shi amma tsaban bala'i haka yake jan ƙafa ɗayan domin ƙari sawa gare su ya sama naman bil'adama kuma ba komai ba ne ya nusar da su da mutane a wurin sai ƙarar motar da Drivern ya ja da kuma ihun kiransa da suke yi.

Wani uban ihu ta kwala tana ja da baya cike da tsoro jikinta babu inda baya rawa take suma sauran suka ankara da abin da ta gani sai dai ruɗani da tashin hankalin da ta shiga ya sa ta kasa tashi daga faɗi ƙasa da ta yi lokacin da ta kurma ihu ai kuwa wani irin super ɗaya daga cikin Zombie'n ya yi tare da kai ma ta wani mummunar cizo a kunne yayin da ɗayan yake wani gurnani yana jan ƙafarsa ɗaya ɗayan kuma shima ɗaya daga cikin ƳAN TIRIRRISHI'n ya kaima farmaki take kuwa ya cije ta duk yadda Mary ta so kwace kanta abu ya cutura har sai da wannan zombie ya ɗayo naman kunnenta tsaban cizo take ta shiga kurma ihun azaba cike da jin raɗaɗi.

“Wayyo Allah Mommy! Kizo ki taimakeni tsoro nake ji wannan wacce irin masifa ce mutane da an cije su sai dai su koma Zombie's gari ya koma tamkar maƙabarta!”

Cikin wani irin matsanancin kuka Miemie take wannan maganar hawaye nayi ma ta zarya kamar ba gobe.

Kallonta Rabi'ah ta yi wannan karon bataji haushinta ba ko kaɗan sai ma tausayi da ta bata hakan ya sa ta ɗan rungumota tana lallashi.

Ganin yadda gadan-gadan Zombie'n da ya cije Mary ya tashi ya nufe su ne yana wani irin gurnani kuma da masifan gudu ya sa suma duk juya suka juya suka fara gudun ceton rai Haleema riƙe da Iya Sahu yayin da Suhaima ta taimakawa Mary ta tashi tsaye haka ma Zieey ta nufa wurin ɗayan budurwar domin taimaka ma ta su gudu sai dai ganin yadda ta fara wani irin gurnani ƙasusuwanta suna bada wani irin sauti jikinta yana makwalkwashewa idanunta sun sauya kala lokaci guda kuma fuskarta ta koma abin tsoro sak irin na zombie shi ne dalilin da ya sa Zieey ta tsaya cak cikin matsanancin faɗuwar gaba ta fara ja da baya ganin yadda a wani karkace kuma ta kwance budurwar da ta koma zombie take tunkaro ta kafin kuma ta wani irin miƙe wa tare da daka tsalle ta cakumo Zieey da niyyar kai ma ta cizo ihun da Zieey ta kurma da kuma ƙarar da ya ninka wanda Zieey ta yi wanda wannan zombie ɗin da ya ciza Mary da kuma mai shirin cizon Zieey suka saki lokaci guda ne ya dakatar da kowa daga gudun da suka fara jinin da ya tallatsa ya wanke fuskar Zieey sakamakon harbin Zombie'n da a ka yi a ka shi ne ya sa Zieey kusan suma cikin dauriya ta cillar da Zombie'n da ta ɗafale ma ta tana wani irin zaro ido kafin lokaci guda su gaba ɗaya suka ɗaga kai domin ganin mahalukin da ya yi ma waɗan Zombie's harbi irin na kwarewa a kai da  lokaci guda suka mutu sai kuwa suka yi karo da shi tsaye sanye da t-shirt da wanda sai backpack da ya goya hannunsa riƙe da bindigar da ya yi amfani da ita gefensa kuma wani Matashi ne shima tsaye sai dai da gani kasan a tsorace yake lokaci guda kusan mutane huɗun nan wato Iya Sahu da Haleema da ma Uwani da Ƴar Gwal suka haɗa baki wurin faɗin.

“Kawu Iliya.”

Yayin da a daidai lokacin zuciyar Rabi'ah dana Suhaima ta yi mummunar bugu na ganin Matashin da ya yi harbin can ƙasan maƙoshi Rabi'ah ta furta.

“Sadiq S Sulaiman?!”

Ita kam Suhaima sai cewa ta yi a fili.

“Abbakar Sadiq?”

A tare daga shi har Matashin dake gefansa da su Iya Sahu suka kira da Iliya suka kalle mutanen wurin sai dai an rasa mai magana sai kallon kallo kawai da a ke yi ita Haleema ma sai da taji Suhaima ta ce Abbakar Sadiq sannan ta gane shi ba kowa ba ne dai fa ce Sadiq S Sulaiman senior ɗin su ne ita da Rabi'ah tun suna secondary school kuma first love ɗin Rabi'ah kafin daga baya suyi break-up dalilin halayensu da suka sha banban kuma tun daga secondary school basu ƙara haɗu da shi face to face ba, ita dai Haleema ta kan ji labari sama-sama a kan sa ita kam dama Rabi'ah ko son jin sunansa batayi.

“Jesus na shiga uku na ni Mary Mum ki taimakeni wannan abu ya cijeni shikenan nima zan zama kamar su zan koma zombie yeh yeh yo!”

Ihun da Mary ta kurma tare da faɗin hakan shi ya mayar da hankalinsu gareta sai lokacin suka lura ashe ma waya takeyi ko kafin, wata cikinsu ta ce wani abu nan ta shiga labarta ma wacce take waya ɗin da ita abin da yake faruwa nan suka fahimci Mahafiyarta ce da yake tsaban ruɗe wa a handsfree ta saka kiran shi ya sa raɗau su Haleema suka ji abin da maman nata ke cewa. Cikin kuka Maman ta ce.

“Jesus, kina jina ko Mary ki kashe kanki kawai dan ba zan so jin kin koma zombie ba hankalina zai fi kwanciya idan a ce kashe kanki kikayi tun kafin ki koma zombie...”

Ganin yadda Mary ta yi tsitt da alama tana tunani a kan abin da mahaifiyar nata ta ce ne da kuma yadda take kallon bindigar dake hannun Sadiq ya sa cikin zaro ido da tashin hankali Haleema ta shiga girgiza ma ta kai tana yi ma ta alama da hannu a kan kar ta yi hakan sannan ta buɗe baki da ƙyar ta ce.

“Dan Allah Mary ki saurareni kar kiyi haka har yanzu fa baki koma Zombie'n ba ki jira mu gannn....”

Jinin da ya tallatsa ya wanke ma ta fuska shi ne ya dakatar da ita daga maganar da take yi domin kuwa Mary ko saurarenta batayi ba sai ma girgiza ma ta kai da ta yi tana hawaye sannan cikin shammata ta ƙari sa tare da wafce bindigar hannun Sadiq ko kafin su yi wani yunƙuri tuni ta saita bindigar saitin kanta sannan ta matsa kunamar take harsashi ya fasa kanta da hakan ya sa jini tallatsa ya wanke fuskar Haleema.

Wani irin zaro ido Haleema ta yi cikin tsananin tashin hankali kafin kuma ta fara  ganin komai na Duniyar ya fara sauya ma ta wani irin jiri dake barazanar zubar da ita ya sa ba shiri ta zube a saman gwiwowinta tana mai fashewa da wani irin kuka da yake fitowa tun daga ƙasan zuciyarta ganin wannan tashin hankalin da take ganin ƙawayen nata sun shiga ne duk a sanadin ta domin da bata matsa musu a kan sai sun zo har nan an yi Tirirrishi ba a ganin ta da duk haka bata faru ba da bata rasa mutane biyu cikin ƙawayen nata ba tsoron ta bai wuce a kan nan gaba kuma su waye kuma har nawa za'a rasa ba shi ya sa ta kasa jurewa zuciyarta wani irin zafi da raɗaɗi takeyi ma ta kuka take yi da dukkan ƙarfinta gaba ɗaya sun yi shiru duk jikinsu ya yi sanyi daga masu hawaye sai masu sheshsheƙa an rasa mai lallashinta har da sai da ta yi iyayinta sannan Rabi'ah da Suhaima suka ƙari sa suna ɗan lallashinta ganin zata iya samun matsala idan ta ci gaba da kukan.
“Rabi'ah, Suhaima bazan iya jurewa ba duk ta sanadina suka rasa ransu yanzu an rasa Mutum biyu nan gaba fa idan kuma na sake rasaku ya zan yi da rayuwata?!”
Haleema ta faɗa cikin kuka.

“Ki kwantar da hankalinki in sha Allahu babu abin da zai sake faruwa.”

Cewar Suhaima cikin lallashi. Ita kuwa Rabi'ah shiru ta yi kamar ba zata ce komai ba sai kuma ta furta.

“Nasan da niyya koma su waye waɗan da suka ƙirƙira wannan bala'i suka yi kuma in sha Allahu ta silar hakan ƙarshensu zai zo domin Allah yana sane da dukkan azzalumai bare kuma marasa imani har haka da za su ƙirƙira Zombie Domin ƙarar da al'umma. In sha Allahu ƙarshen su gaba ɗaya ba zai yi kyau ba azzalumai kawai.”

Gaba ɗaya amsawa suka yi da Ameen kowa da irin mugun fatan da yake yi musu amma banda Sadiq da yake ji jikinsa bai taɓa yin sanyi ba bai kuma ji danasani ba gaba ɗaya sai yanzu yake jin ya matuƙar tsanar kansa.

Ya sauke ajiyar zuciya yana kau da kai.

Bayan wasu mintoci.

Tafiya suka ci gaba a cikin dajin babu mai cewa kowa komai domin har Sadiq zai bi nasan hanyar daban amma sai suka ce ya bisu su tafi tare ganin irin taimakon da ya yi musu.

Tsayawa suka yi lokacin da suka ƙari sa gaban wani irin makeken gida ginin zamani da ƙaton gate a gabansa cikin mamaki Iya Sahu ta riƙe haɓa ta ce.

“Ikon Allah ke nan dai wannan shi ne gidan da muke jin labarinsa...”

“Wani gida ke nan Iya kuma mene ne gidan ya yi wani irin labari kuke ji a kansa?”

Rabi'ah da gidan ya gama tafiya da imaninta ta faɗa tana duban Iya Sahu sai dai tun kafin iya Sahu ta ce wani abu Yar Gwal ta ce.

“Cewa a ke da Fatalwu a gidan kuma GIDAN IKO ma a ke ce masa dama Wallahi ina so naga gidan gashi yau ina tsaye ƙofar gidan.”

“Ke Yar nan raba kanki ai Bama wai ba domin an tabbatar wannan gida Fatalwu Bama ɗaya ko biyu a ciki ba banda hakan mai zai saka a zo ƙaton daji kamar wannan a gina sankacecen gida

irin haka sannan a barshi a ƙi tarewa.”

Iya sahu ta katse Ƴar Gwal tana ƙara ƙare ma gidan kallo.

Gaba ɗaya kallon gidan suke suna jin yadda wani shauƙi na son shiga ciki ya ɗauke su gaba ɗaya burinsu bai wuce su shiga ciki ba.

Taɓe baki Rabi'ah ta yi.

“Ai wallahi ba Fatalwa ba in ma rufanai ne a gidan sai dai su ganni su kyale a to ban da ƙarya irin na mutane ji gida tsaftsaf da shi kuma ginin zamani amma a ce wani Fatalwu ne a ciki nabi Fatalwun da gudu dan ubansu.”

Dariya ta bawa kowa da maganarta duk da halin da suke ciki na jimami.

Iya sahu da ta fara yarda da maganar Rabi'ah ta ce.

“Eh to kuma fa haka ne ji ye min dai ƴar nan ba wani Fatalwu kawai so a ke a tsorata mutane dama shi ya sa a ka daɗe ana yaɗa jita-jita wai Fatalwu ne a gidan.”

Ta faɗa tana kama ƙaton gate ɗin gidan take wuya taji ta ƙara matsuwa da su shiga ciki.

“Dare ya yi kuma babu Wurin kwana ina ga mu shiga ciki kawai da addu'a in sha Allahu ba wasu Fatalwu in ya so da safiya tayi mu ci gaba da tafiyarmu.”

Cewar Muhsin yana jira yaji ta bakinsu.

Gaba ɗaya sun yi na'am da shawararsa hakan ya sa duk suka nufa hanyar shiga gidan gadan-gadan tsaban ƙosawa da zumuɗi ma ko addu'ar basu yi ba shima kansa mai maganar a yi addu'ar ba yi ya yi ba su ka sa hannu a tare suka buɗe ƙaton gate ɗin suka kuwa ci Sa'a a buɗe yake ba kuwa da tunanin komai ba suka antaya ciki....

♡YAN TIRIRRISHI!♡

P.12,13.

Shigarsu gidan keda wuya ƙaton Gate ɗin ya mayar da kansa ya rufe gam, zuwa lokacin da suka shige kuwa ginin gidan ne gaba ɗaya ya fara sauyawa kamar al'mara daga yadda yake gini na zamani mai kyau da burgewa lokaci ƙanƙani ya rikiɗe ya koma tsohon gini irin na zamanin da can yadda kasan ya yi Shekaru sama da ɗari ba'a taɓa shiga ba haka ya koma...
Abuja, Nigeria
Cikin matsanancin tashin hankali take tun lokacin da ta sama labarin abin da yake faruwa na cutar da ta yaɗu mutane suna cizon junansu suna komawa Zombie's gashi a inda Yarinyar ta ɗaya tilo wato Rabi'ah ta tafi nan ne wannan masifar da suka tsinci kansu ciki ya samo asali ga ƙaninta Habib shima da ta tura dan ya saka ma ta ido a kan Rabi'ah'n tun samun wannan mummunar labari take faman kiran shi amma amsa ɗaya ne layin sam baya shiga shi ya sa gaba ɗaya ta ruɗe duk ta fita hayyacinta, ba tare da ɓata lokaci ba kuwa ta yi amfani da ƙarfin ikon da take da matsayin ta na General na Sojoji wurin saka doka mai tsauri a kan ganin wannan cuta da mutane ke zama zombie bata shigo Abuja ba gefe guda kuma ta ware sojojin na musamman suna shawagi a yankunan da wannan al'amari ya rufta da su da kuma saka ido domin ceto waɗan da wannan cuta bata ritsa da su ba gefe guda gagarumin zama na gaggawa da gwamnati ta shirya a kan wannan al'amari ta tafi a inda suka tattauna a kan yadda za'a ɓullo wa lamarin duk da abin akwai ɗaure kai domin har zuwa lokacin basu san ta ya a ka yi wannan abu ya samo asali ba....
Ɓangaren Mahaifiyar Amarya Haleema kuwa kusan zaucewa za'a ce Mama da Hafsa dama sauran ƴan uwa suka yi lokacin da suka sama labarin abin da yake faruwa bare kuma shi kansa ango da ya fita hayyacinsa ƙarin tashin hankalin kuma shi ne da ko'a waya basu sama Haleema ba bare susan halin da take ciki.

Ɓangaren su Haleema kuwa lokacin da suka shige cikin gidan wani irin ƙayataccen haɗaɗɗen palo na ban mamaki suka tarar wanda ya basu mamaki dan da farko sai da suka ɗan tsorata ganin haɗu war palon duk da dai ba'a cikin hayyacinsu suke ba sakamakon abin da yake faruwa.

“Ni Ƴasu ina ne nan muka kawo kanmu kuma an ya bamuyi kuskuren shigowa gidan nan ba kuwa?”

Iya Sahu ta faɗa tana riƙe haɓa.

“Haba dai ji gida har gida ai ba wani abu kar ma ki tsoratar damu bari ma ki gani na ga kamar kitchen ne a can bana duba ko'a sama abin da taɓa wa dan cikina har wani kiran chiroma yake”

Zieey ta bawa Iya Sahu amsa tana shigewa kitchen dake gefe, yayin da Rabi'ah da bata kai ga zama ba kamar sauran saima ƙare ma palon kallo da take yi a nazarce ta ce.

“Bara na duba ko zan ga Toilet.”

Ta faɗa tana yin gaba, yayin da duk sauran suka zazzauna suna hutawa da kuma tunanin abin da za su tarar nan gaba dan hankalinsu ba wai ya kwanta ba ne ba, shi kuwa Habib fita daga palon ya yi yana danna waya dan yaga Akwai network so yake ya samu ya keɓe ya kira mahaifiyar Rabi'ah Wato General ya sanar da ita suna cikin ƙoshin lafiya.

Lokacin da ya kira layin nata kiran farko ta ɗa ga cikin tashin hankali take tambayarsa halin da suke ciki dan saboda tsananin ruɗe wa ma kuka ta saka ta kasa nutsuwa ta saurari abin da zai ce ma ta sai da ƙyar ya samu ta nutsu shi kuma sai da ya kwantar ma ta da hankali sosai sannan ya faɗa ma ta Dukkanin abin da yake faruwa da halin da suke ciki kuma daga ƙarshe ya tura ma ta location na wurin da suke acewarta kar ma ya yarda suyi kuskuren fita daga gidan domin sojoji zata turo a helicopter domin taimaka musu zuwa Abuja'n domin an saka tsoro sosai yadda masu cutar ma'ana Zombie's ɗin ba za su iya shiga Abuja ba dama sauran States ɗin da abin bai shafa ba kuma likitoci kwararru suna iya kar bakin ƙoƙarinsu dan ganin an samo maganin wannan cuta.

Sai da ya sauke ajiyar zuciya na samun nutsuwa lokacin da ya sauke wayar sannan ya juya da nufin komawa ciki sai dai cak ya ɗan ja tunga cike da mamaki yake kallonta tsaye gabansa tana sakar masa murmushi, ɓoyayyiyar ajiyar ya sauke dan kuwa ta bashi tsoro saboda bai taɓa zaton da mutum a bayansa.

“W-wani abu kike nema?”

Ya tambaya yana ɗan kallonta ganin ta zuba masa ido shiru ta yi masa saima ci gaba da kallonsa da take kamar ma bataji abin da ya ce ba har sai da ya sake magana sannan ta yi firgigit tana dubansa baki washe ta ce.

“A-ah d-dama fa abinci na kawo maka.”

Cike da mamaki ya dubeta da kular da take miƙo masa sai ma kuma ya nuna kansa cikin nuna zallar mamaki ya ce.

“Abinci, ni kuma?”

“Eh mana nasan kana jin yunwa shi ya sa na kawo maka karɓa.”

Ƴar Gwal ta yi maganar tana sake miƙa masa. Tana kuma tuna yadda tayima Uwani wayau ba tare da ta sani ba ta ɗauke abincin ta fito.

Rabi'ah...
Da sauri ta mayar da ƙofar toilet ɗin ta rufe lokacin da ta shiga ciki tana sauke ajiyar zuciya sai da ta tabbatar da ta sama nutsuwa sannan ta buɗe idanunta dake lumshe tana zaro hannunta da ta ɓoye a baya kamar wani ya ce zai gani ta yaye dogon hannun rigar jikinta a take sawun

cizo da haƙuri ta bayyana, ajiyar zuciya ta sauke tana tuna lokacin da ta sama wannan cizo, a lokacin bayan ta saka Habib ya koma domin ceton Ƴar Gwal ita kuma sai ta fito daga motar ta tsaya tsaye tana jiran dawowarsa cikin shammmata kuwa Zombie'n da sam bata lura da shi ba ya kai ma ta hari sai dai ta yi saurin an kara sai dai duk yadda taso ta tare kanta abu ya cutura har sai da ya sama nasarar cizonta sai dai sam bata lura ba har sai da wurin ya fara yi ma ta zafi lokacin da suke kan hanyar ƙari sowa wannan gida sai dai tana mamakin duk tsawon wannan daɗewan da ita ba zama Zombie'n ba bayan kuma ba'a haure minti guda da zarar Zombie'n ya cije ka kai ma zaka zama kamar shi, ƙura ma kanta ido ta yi ta madubin toilet ɗin kafin ta fashe da wani irin kuka dan bata da abin yi sama da hakan sai da ta yi ma'ishi sannan ta wanke fuskarta tana ci gaba da kallon kanta a madubin a take kuma tass! Kakeji Madubin ya tarwatse da hakan ya sa ta ja baya cike da mamaki da kuma ruɗani dan ita dai tasan bata taɓa ba kuma bata ga komai ya taɓa ba amma kuma madubin ya fashe da kanshi ko kafin ta yi wani yunƙuri wani irin ƙara marar daɗin saurare ya karaɗe gaba ɗaya gidan da hakan ya sa ta yi saurin toshe kunnenta gudun kar ƙarar ya yi ma ta illa sai kuma ta fito daga kitchen ɗin a guje ta ƙari sa palon ta tarar da wani tashin hankalin gaba ɗayansu ta gani tsay-tsaye cikin matsanancin tashin hankali sun yi ma tsakiyar palon zobe da alama wani abin na tashin hankali suke gani.

“M-me nene yake faruwa anan?”

Ta tambaya a ɗan rikice tana ƙoƙarin ƙari sawa wurin da mugun sauri Haleema ta ƙari sa tare da tararta cikin wani irin yanayi take faɗin.

“ba wani abu fa ba sai kin gani ba.”

Kallon rashin yarda Rabi'ah tayima Haleema kafin ta mayar da akalan kallon nata a kan Suhaima da idanunta ya yi jajur ga kuma hawaye da yake faman zirya faman fuskarta kamar an buɗe famfo.

Slowly Rabi'ah ta mayar da idanunta a ƙasa wurin da suke kalla lokacin da ta ƙari sa wurin, wani irin bugawa na tsananin tashin hankali zuciyarta ta yi tana wani irin tsinkewa tare da zillo yadda kasan zata fito waje lokacin da idanunta suka sauka a kan Sadiq dake kwance baya numfashi alamar babu rai a tare da shi ga jini dake fita daga kanshi yana malale wurin, wani irin juwa ne da ya kwashe ta da har ya kusa kaita ƙasa tana ci gaba da kallon gawar Sadiq ɗin cikin wani irin tashin hankali kafin cikin wata ruɗaɗiyar murya da kuma sarƙewar muryar lokaci guda ta furta.

“M-m-me ne ne yake faruwa anan garin ya ya hakan ta kasance.”

Ta faɗa tana kallon su da jajayen idanunta Habib da ya ƙari sa wurin da niyyar taimaka ma ta ta

miƙe ne ya furta.

“Ƙarar faɗowarsa daga saman bene kawai mukaji all of a sudden ba tare da sanin dalili ko mafarar hakan ba....”

“Muyi gaggawar barin gidan nan domin ina iya jiyo alamun muggan halittun da suke ciki kuma da alama sune suka yi silar da ya faɗo har ya mutu tabbas mun yi kuskuren shigowa gidan nan...”

Iya Sahu ta faɗa cike da tabbatar da kalamanta ta hanyar nuna tashin hankali ɓaro-ɓaro saman fuskarta.

Cike da tashin hankali duk suke kallonta jin abin da ta faɗa ta kuwa sake tabbatar musu da kalamanta ta hanyar ɗa ga musu kai alamar tabbatar wa.

Cikin wani irin tashin hankali kowanensu ya nufa ƙofar palon domin fita daga gidan ko sa tsira da rayuwarsu duk da suna da tabbacin idan suka fitan ma ba wai sun tsira bane wani tashin hankalin ne yake can yake jiransu wato Zombie's.

Sai dai kwatsam suna ƙari sawa wurin ƙofar ko kafin su sama nasarar fita da ƙarfin tsiya ƙofar ya mayar da kanta ta rufe lokaci guda kuma gidan gaba ɗaya ya fara wani irin girgiza yayin da wasu kalan muryoyi suka karaɗe ko'ina na gidan cikin muryoyi marasa daɗin ji ake wasu gwalan-gwalan da sam basa iya fahimtar abin da ake faɗa ban da zaro ido da ƙanƙame juna cikin tashin hankali ba abin da suke yi gaba ɗaya tsaban tashin hankali sun ma kasa addu'a zuwa can juyawa da ƙarar tarwatsewar gilashi da gidan yake yi ya dakata haka ma waɗan nan muryoyin kafin kuma wata kakkaurar murya ta karaɗe dukkanin palon tana kuma amsa amo a gidan dama dajin baki ɗaya.

“Tabbas kun kawo kanku gidan mutuwa inda ba'a shiga a fita haƙiƙa kun yi kuskuren kawo kanku cikin Masarautar mu wato Gidan iko sai mun ga bayan kowannenku kamar yadda muka ga bayan wannan la'anannen.”

Muryar marar daɗi da ta karaɗe palon ta ƙare maganar ana yi musu nuni kuma da gawar Sadiq da ke gebe duk da basu san ta inda mai maganar yake ba ko kafin kuma suyi wani yunƙuri sai ga bidiyo ya bayyana a tsakiyar Palon saman iska bidiyo ne na Sadiq da Daniel Jack lokacin da suke arguing a kan abin da Sadiq ɗin ya yi na haɗa kai da turawa har zuwa lokacin da wannan Zombie'n ya fasa gilashin ya kuma kai ma Daniel Jack farmaki da zuwa lokacin da Sadiq ya gudu a wurin.

Basu gama shan mamaki da ganin wannan bidiyon ba sai kuma ya yanke a ka ƙara wani shi kuma Suhaima ce tare da Sadiq a bidiyon suna waya ne a kan bikinsu da ya kusa domin an saka musu rana daga haka kuma bidiyon ya yanke wannan murya mara daɗi ta ci gaba da faɗin.

“Saboda haka ya cancanci ya mutu shi ya sa muka kashe shi mutuwa mafi ƙasƙanci...”

“Baku da ikon aikata hakan dan kawai ya aikata abin da ya aikata sai kuma a ka ce ku kashe shi hukuma ita ce zata yanke masa hukunci kafin yaje ya tarar dana Ubangiji baku ba aljanu kuma idan ma haka ne mun yarda shi mai laifi ne shi ya sa kuka kashe shi amma mu kuma fa laifin miye mukayi muku da kukeson kashe mu....”

Wani irin dunƙulallen iska ne ya ɗauke Rabi'ah dake maganar ya yi sama da ita kafin kuma a ka saukota ƙasa a ka yasar a tsakiyar Palon ta saki ƙara na azaba tana dafe bayanta da hakan ya zama sila na ganin cizon dake hannunta da suka yi cikin zaro ido da tashin hankali ɗaya daga cikin ƴan matan ta ce.

“Cizon miye a hannunki Rabi'ah kar dai kice kema Zombie'n ne ya cije ki?”

Budurwar ta faɗa cike da tsoro tana ja da baya, da sauri Rabi'ah ta rufe Wurin cizon idanunta a ƙasa ta ce.

“kuyi haƙuri nima ban lura ba sai...”

“me kike nufi da muyi hakuri iyyye so kike kamar yadda a ka cijeki zaki zama zombie muma mu bari ki cije mu ko me.”

Kawu Iliya ya faɗa a hasale, cikin tsananin damuwa Rabi'ah ta basu labarin ainihin Yadda akai har aka cijetan kuma bada niyya ta ɓoye musu ba sai dai tun kafin ta rufe baki Muryar aljanar nan ta katseta da faɗin.

“kema kuma kin zama maci amana saboda haka sai mun hallaka ki domin alƙawarine mukayi duk wani maci amana ba zamu kyaleshi ba har sai mun ga bayanshi domin muma amanar mu a ka ci a ka rufe mu a wannan kurkukun gidan tsawon shekaru masu yawa saboda haka duk wani maci amana ko kuma wanda ya kawo kansa wurin mu ba zamu taɓa barinsa da rai ba...”

“ƙarya kuke yi domin baku isa ku cutar damu ba domin kuwa mun riƙe Allah kuma mun fi ƙarfin ku kuma babu abin da kuka isa kuyi wa Rabi'ah tun da ba ha'intar mu ta yi ba. Kuma sannan da'a ce zata zama Zombie da tuntuni ta zama saboda haka tun da ta kawo wannan lokaci ba ta zama ba hakan na nufin ita ɗin TA DABAN ce ba zata taɓa zama Zombie'n ba..”

Muryar Iya Sahu cike da rashin tsoro ta katse su da faɗin hakan cikin hargowa, sannan ta dube mutanen wurin cikin kwarin gwiwa ta ci gaba da faɗin.

“kada ku bari wannan aljanar ta yi nasara a kan mu mu yita addu'a har Allah ya bamu ikon fita daga gidan...”

Cike da kwarin gwiwa duk suka amsa ma ta kafin su fara addu'a daga sun gama wata suke kama wata da fari dariyar shaƙiyanci aljanar ta sheƙe da shi amma zuwa wani lokaci da suka ci gaba da Addu'o'in ba saurarawa sai ta fara roƙonsu a kan su tsaya saboda suna ƙonata suna kuma cutar ma ta da yara da Masarautar ta amma su ka ƙi saurararta sun kusa awa guda suna karon ba gajiyawa duk da lokacin dare da ya yi sosai ga kuma gajiya da yunwa a tare da su amma haka suka daure suna ci gaba da karanto Addu'o'in ai kuwa kamar al'mara suka ga an yi jifa da su sai gasu sun bayyana a tsakiyar gidan cikin tsananin farin ciki ba kuma tare da sun dena karatun ba suka tashi a tare har da riƙe hannu suka ƙari sa wurin Gate ɗin nan ma suka yi masa ƙawanya wasu suna bubbugawa wasu suna ci gaba da karatun gaba ɗaya sun fita hayyacinsu zuwa lokacin da yake suma aljanun ƴan taurin kai ne sai suka fara tsoratar da su amma duk da hakan suka daure suna ci gaba da karatun idanunsu a rufe saboda kar ma suga abin tsoron da a ke nuna musu, sun ɗan ɗauki lokaci mai tsawo a hakan kafin kamar a mafarki sukaji ƙofar ta buɗe a tare kuma cikin wani irin yanayi suka buɗe idanunsu suna masu takawa wurin fita daga gidan ai kuwa sukayi kiciɓis da wasu daga cikin sojojin da General ta aiko sun ƙari so da jimawa sunata shawagi a wurin suna nemansu da basu gansu ba har sun fara shirin komawa cikin helicoptern nasu subar wurin sai kuwa cikin ikon Allah sai gasu Rabi'ah sun sama nasarar fitowa daga gidan iko lokacin da suka ga helicoptern dake sama har uku da kuma sojojin sai suka sauke ajiyar zuciya domin sun fahimci wahala ce ta ƙare musu za'a taimaka musu a fili suka haɗa baki wurin faɗin “ALHAMDULLILAH”

______
MA SHA ALLAH

KUMA ALHAMDULLILAH ALHAMDULLILAH ALA KULLI HALIN....

Anan na kawo ƙarshen wannan taƙaitaccen labari nawa mai taken ƳAN TIRIRRISHI ina fata mun ƙaru da abubuwan dake ciki Allah ta'ala ya sa mu dace a gurguje dai mu haɗu a littafina da zai fara zuwar muku cikin satin nan da yardar mai duka mai taken BA RIBA, (there is no other choice 🔥) ku jira fitowarsa kawai domin littafin na daban ne ko daga jin sunan ma ba sai an

faɗa ba.🤗

NainarhKDnkd's ✍️
07067953066
Or
08081129487
Tue,May, 20. 2025.
Thank you Again...❤️